💫 FARRAH💫

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

1️⃣
KAUYEN KUDURI
Babban rapi ne sosai da ruwa ke gudana aciki yana kaida kawowa, ruwan rafin gashinan ja kalan kasa, ta baki bakin rafin kuma duwatsu ne manya manya da kanana kanana masu kyau ruwa na zuwa na hawa kansu yana komawa, ga mataye manya da yara sama da su dari duk an kachame gaban rafin ana wanki yanda kasan gasan wanki akeyi ana hayaniya ana wake, wani dankwaleliyan rana da ake kodawa daya fito mai zafin gaske ya haska ko'ina hakan yakarama wajen kyau.
Zauna kan wani dutse wata yar matashiyan budurwa take ga uban kaya agabanta data wanke gakuma wasu masu uban yawan a gefenta da batariga ta wanke ba, ahankali zufa ke gangarowa daga gefen fuskanta suna diddiga acikin ruwan, wasu yan mata guda biyu ne tsaye kan dutsen abayanta suna sanye da zani daban riga daban sai wani koren dan kwali akansu hannayensu duka rike da rake sunasha suna kalle kallen sauran matayen dake wanki awajen, daya daga cikinsu ne tace “Rakiya wlh muzamuci wanan gasar, kalli su Lami da Tani ko rabin wankin nasu basuyi ba” wacce aka kira da Rakiya juyawa tayi ta tofar da raken dake bakinta sanan takalli wacce ke zaune agabansu data basu baya tana wankin kayan tace “wai ke barakiyi sauri ba Farrah saisu Tani sun rigamu” kara saurin wankin tayi batare datace uppan ba, Rakiya taja tsakin takaici takalli kawartata tace “wlh kaman nakashe yarinyar nan nakeji, saina tabbatar dana wulakanta ta akauyen nan Atine” zubar da tsakin bakinta Atine tayi tace “yo wulakantawa kuma na nawa meya rage? Bayan kun riga kun kurmantar da ita, gashi kuma tariga tazama jakan gidan ku” ta tabe baki tana kallon bayan yarinyar tace “ke kiyi dasauri ko wlh barakici abincin rana dana dare ba duka kinsan halin yan gidan dakike” duk maganan dasukeyi tanajin su bata cemusu komi ba sai kara saurin wankin datayi tagaji tun safe wani safe tun jiya bakinta baiga abinci ba aiki kawai takeyi, duk suna tsaye awajen bata kara minti talatin ba takarasa wanke uban tulin kayan dayarage tass dayake Allah ya yita da zafin nama, kaman jira suke tagama wani kalan hankadeta Rakiya tayi tafada cikin rafin tsundum Rakiya tadauki kayan data wanke itada Atine sukahau ihu suna mungama wankin mu, matan wajen suka bisu da kallo ana hayaniya kaman basune suka hankada mutum a cikin ruwa ba, ahankali taciro kanta daga cikin ruwan tasa hannu tashare fuskanta ahankali tana bude idanun, wasu kalan fararen idanun takedashi tass kwayan idanunta kuma light brown ne ba baki ba, giranta acike fam da gashi baki sidik dake neman hadewa duka biyun, goshinta gabaki daya gashi ne dasuka kwanta sabida ruwan data fada, ahankali takebin kowa da kallo yanda su Rakiya ke tsalle suna

murna sunzo na farko agasan wankin anjima zasu karbi kyauta wajen mai gari dawani tukuici na musamman, gently tafito daga ruwan sanan tamike tsaye ahankali, ko kadan batada wani tsawon kirki, itadai bazaka kirata da gajera ba sanan baraka kirata da doguwa ba dan batada tsayi ko kadan gashi batada kiba kaman ka hureta tafadi, dariyan dataji anayi yasa tadan juyo su Rakiya ne da kawayenta kemata dariya suna nunata, daya daga cikin kawayen su Ladidi tace “da idanuwanta kaman na mussa” suka kara kwashewa da dariya, Rakiya tace “wada kawai kurma” dasauri ta wuce tana tafiya dasauri sauri duk inda tabi ana kallonta ahaka hartakai gidan su acikin kauyen, gida ne matsakaicin gida na kasa, tura kyaure tayi tashiga cikin gidan gidan fess fess babu kowa gidan tasan Inna nachan gidan mai gari yaran gidan kuma koba’a gayamata ba ta tabbata suna chan rafi, wajen garken tumakan gidan da shanaye tayi sanan ahankali ta tura wani kofa dake wajen daya sadata dawata Yar karaman daki dako Leda babu akasan dakin sai uban jan kasa dake kasa, babu komi adakin sai wani bakin zanin gado dake chan gefe da alamu nan ne gadonta ashimfide akasa sai wani kullin zani dawajen tayida saurinta ta warware wata kodaddiyar doguwan Riga tadauka agurguje tacire na jikinta ta saka sanan ta dauko wani hula ta cire hulan kanta daya jike wasu dogayen gashi suka zubo har wajen waist dinta tattare gashin tayi ta tura a hulan sanan tafito ta shanya kayan kan igiya sanan ta tsaya chak tabi gidan da kallo cikinta nawani irin kukan yunwa, komawa da baya da baya tayi ta jingina da bango ahankali tana kallon kitchen dinsu da aka zagaye da langa langa, takai kusan minti biyu ahaka sanan ta tsugunna ahankali jin kaman zata fadi tana kallon kitchen din still, yunwan datakeji jitake kaman ko mutum aka bata yanzu hakan nan zata iyaci, bakinta har wani rawa rawa yake fararen idanunta na juyawa sosai, ganin kaman zata mutu yasa taji wani kalan karfi yazo mata tai kitchen din dagudu tana zuwa ta bude tukunyar wata shinkafa ce dafa duka datai jajir kaman ansamata color atukunyar wani irin yawu taji ta hadiye cikinta yay wani kalan kugi na yaga abinci, batasan lokacin da marfin tukunyar hannunta yafadi kasa ba tasa hannunta cikin tukunya ko kadan bata damu da zafin abincin ba tashigaci kaman wacce tai shekaru aduniya bata sami abinci ba.

Sallaman Inna dataji atsakar gidan yasa gabanta yay wani kalan mummunan fadi dawani irin bala’in sauri ta tashi daga gaban murhun tana komawa da baya da baya bakinta duk manja hakama hannunta bama tasan ina zataba tsabagen yanda jikinta kerawa, duk duniya babu wanda take tsoro kaman Inna, ko muryanta taji jikinta kyarma yake, cin karo datayi da uban tukwane dake jere a kitchen din yasa suka watse sukai wani uban kara dayasa Inna dake tsakar gida tana cire hijabi tace “waye agidan nan? Ina baduka yaran nan suna rafi ba” tai maganan tana yin hanyar cikin din chak ta tsaya ganin marfin tukunyar abincin su akasa gakuma Farrah dakeyi kaman zata binne kanta cikin tukwannen dasuka baro akasa jikinta na bala’in kyarma tana kallon Innan dake wani irin kallonta da mugayen idanunta tanabin bakinta da hannayen ta da Farrah tashiga gogewa ajikin riganta da kallo, cikin wata irin bakar rai tace “yanzu kuma sata kika faramin Farra’u? Wato gudowa kikayi kika dawo gida kowa nachan rafi eh? In ciyar da ubanku sanan inciyar dake Yar ruko, Farrah nine fa Inna Basira kin manta wacece ni”? Wani irin bayanta Farrah tashiga bugawa ajikin bangon datake tsaye kaman ginin yafadi takeji tabi tagudu hawaye yashiga saukowa daga idanunta tana girgiza mata kai, juyawa Inna tayi tashige wani daki dake nan inda take tsaye bata wani jimaba tafito rike dawata zaftareriyan adda tace

“ai kin tuna wanan addan ina? Wlh wlh wlh yausaina kasheki” tai inda Farrah take tsaye, wani kalan ihu na kurmaye Farrah tashiga yi dayar siriruwan muryanta dabayama fita da kyau, duk duniya batada abinda take tsoro kaman Innan su, duk inda taganta takan mata kallon dodo ne ma, kafin takai wajen kawai ta sume, cikin fushi Inna tace “wlh ko mutuwa kikayi sainasa kinyi na biyu” tadaga addan zata chakamata kaman daga sama taji an kwalamata kira. “Basira! Basira! Basira! Sau nawa nakiraki” chak tajuyo jin muryan Malam dan batazaci yana gida ba, wani dan siririn magidanci ne yafito, idanunshi sundan tashi sun kumbura da alamu bacci yasha, hannunshi rike da buta yana tsaye bakin kofa yana kallonta girgiza kai yayi sanan yakai bakin buran zuwa bakinshi ya tsayaya ruwa sanan yasauke hannunshi kasa ya kuskure bakinshi sanan ya zubar da ruwan kafin yasake kallonta cikin harshen shi dababu hausa sosai yace “ina gujemiki hukuma Basira, ina gujemiki hukuma amman bakiji, babadan matan megari dasuka rufamiki asiri sukasa mai gari yama yan sanda magana ba da yanzu kina chaji offis, amman ga fili gamai doki baran hanaki ba ki kasheta, bismillanki” yay maganan yana zare mazagiyar wandonshi da hannu daya yana tafiya zuwa hanyar bayi, cikeda fushi dakuma cin mutunci tace “malalacin miji kawai, kullum baka da aiki sai baccin banza daga safe har dare kana turaka nadafa nabaka barakaje nemaba, ahaka kuma ka kawomin yara, in ciyar dakai na ciyar dasu tunda gani banza ko bansan ciwon kaina ba” fitowa yayi daga makewayen yana binta daga ita har Farrah datake asume dakallo yace “kinga nahanaki nace karki kasheta? Banfa ceba duk yanda kikaga dama kiyi ai gamai fili gamai doki, inda kina bata abinci zata miki satan abinci ne, wanke muku jiki ne kawai yarinyar nan batayi agidan nan Basira, kodan uban aikin datake muku ai kya ciyar da ita” cikeda fada ta taho inda yake duke zai fara alwala tace “Malam kai meya hanaka ciyar da ita? Ina diyar kanwanka ce da akawa cikin shege eh, daga zuwa tasha saida nono tafara karuwanci aka duramata cikin su, wlh kafita daga idanuna Malam inba hakaba kaima nakusa koranka daga gidan nan mara zuciya kawai, na mace” mikewa tsaye yayi yana wanke kafa sanan yatashi yana addu’a kafin yakalleta yace “idan kin isa ki koran nagani shedaniya kawai” ihu tayi tana tafi tace “gaka nan babban shaidani mai matacciyar zuciya, kana kwance ni zan fita nema, daidai da kayan jikin ka nina siyamaka akasuwan gabari, dawo kaciremin silipas dina ai nina sayo na kafan ka” juyowa yayi ya wurgamata harara sanan yabude kyaure yawuce yafita itakuma tajuyo tana kallon inda Farrah take azube asume tana kara kallon addan data Yar akasa tai kwafa, tasan maganan malam gaskiya ne saisa kawai tafasa kasheta amman ta tsani yarinyar nan ta tsaneta ta tsaneta she wish zata iya kasheta taje ta Yar batare daya tada tambaya ba datayi hakan wlh, komawa dakin data ciro addan tayi ta ijiye sanan tafito takoma dakinta tazauna tana karkada kafa.

Shigowa gidan yayi bayan yay sallan la’asar, Farrah dake kwance asume inda take a kitchen yabida kallo yana tafiyan nan kaman iska zai kwasheshi yafadi tsabagen rama sanan yashiga dakin, Inna dake zaune atsakar falon ta bishi da mugun kallo dan kaman tashakeshi takeji, wata Yar karaman radio dake kan Yar kodaddiyar tv su yadauka yana jawo antenna radio waje sanan ya kunna yana murza tasha yana kokarin kamo tashar BBC, Inna dake ballamai harara tace

“tirrr wlh kayi asara arayuwanka mai mataccen zuciya kawai” sake tabe baki yayi sanan yadauki taburman dake nannade an jinginar dashi a tsaye gefenta yawuce yafito cikeda cin zarafi da mugun son yakulata tace “nagadai tabarman ma tawace nina saya mara zuciya” shimfida tabarman yayi agaban dakin sanan ya ijiye radio yamike tsaye yasake kallon Farrah a inda take sanan yawuce butanshi dakenan inda yabarta anan tsakar gida dazun dayay alwala yakarasa yadauka dayake da ragowan ruwa aciki yana kara girgiza butan dan gane iya ragowan ruwan dayake ciki sanan yawuce inda take ya tsaya a kanta dan kallonta ya tsaya yanayi yay jim kaman mai tunanin wani abu rabon da yadaura idanunshi akanta wlh yama manta hakanan ganin fuskan marigayiya kanwarshi yayi kaman ita lokacin datana sa’an Farrah, girgiza kanshi kawai yayi sanan yadaga butan yashiga tsiyaya mata ruwan ciki kan fuskanta yana kiranta. “Ke, Farra’u, ke!” Yakirata da karfi ahankali tashiga motsi tana yatsine fuska jin ruwa akanta saikuma kaman wacce aka tsungula tawani mugun zabura tamike tana kara wargaza tukwanen dake wajen tana ihun kurame dayar muryanta, Malam daya bita da kallo yace “zakici gidan ku ne, da idanuwanki kaman na shaidanun ruwa, ko agidan wa kika koyo sata kije ki zubar dashi gidan nan kasheki zasuyi kikace sata zaki dinga musu, yo ke bakima tausayin kanki Iyye, jibi jikinki babu nama kodaya, bakida suturan arziki, tsabagen bakin wahala abinci sai wanda aka yammiki kuma kice zaki dingawa masu ciyar dake sata, Farrah anya kinason kanki kuwa da zaman lafiya”? Gyadamai kai tayi ahankali tana goge hawayen dasuka zubomata da bayan hannu kanta akasa dan itama bata iya kallon Malam, binta yayi da kallo daga sama har kasa yace “wuce ni ki zubamin abincin naci kirufe tukunyar dakika yadda marfin akasa” kaman jira Inna take azuciye tafito daga dakin tazo kitchen din tana tafi tace “wlh bazaka cishi ba Malam, mai tauraro kasayamin koko ajino moto eh? Sule biyar dinka babu a abincin nan dan haka wlh barakaci shi ba, kekuma dan ubanki kwarto dahar yau baki sani ba idan kin isa kitaba abincin nan kiga idan ban guntule wayan nan fararen hannuwan naki ba” dukawa Farrah tayi tana sunnar da kanta kasa tana kulle idanu jikinta na kyarma bala’in tsoron Inna take, inhar tana gidan batada kwanciyan hankali, dan kallon Inna Malam yayi sanan yadan saci kallon tukunyar yanda yaga shinkafar tai jajir yaji ranshi yakara biyawa bazai iya mata zuciya ba cikinshi yashiga kugi, dan murmushi yayi yakalli Inna yace “wai Kodai yau matan mai gari basu biyaki kudin aikatau bane naga ranki abace ne Basirata” harara ta ballamai tace “kanka akeji munafuki” tajuya zata wuce dasauri ya chapke hannunta cikeda muryan lallashi da lallabawa yace “yakuri dan Allah ki zubamin shinkafar nan wallahi yunwar tsiya nikeji” fizge hannunta tayi tace “bakariga kajita ba, bani kazauna kake gaggayama maganganu ba sabida wanan shegiyar kurman beben yarinyan dabata da amfanin duniya balle nalahira yanzu ai saikaci babu kokuma ita taje tanemo tadafa tabaka kaci” gabanta yasha dasauri yakalleta cikeda so yace “haba mana Basira, naface kiyakuri fa, kizubamin naci fita zanyi naje wajen Luku zandawo da kudi kinji” dauke kai tayi tareda rungume hannayenta aciki, washe baki yayi ganin yasoma shawo kanta yace “haba surukan Mai Gari, Maman mai farin jini ke bakiga yanda akema yarmu Rakiya layi ba, saisa nima nai na’am da dan Mai Gari zata aura kaman yanda kika fadi, yarinyar ki saidai mahassadi eh Yar matata, bakiga Rakiya ba jajur da ita uwa hurun ini” wani kalan washe hakora Inna tayi tace “yo ai har yanzu batakai Farrah ja ba saisa nasayo mata wani mai akasuwan gabari nasa tana shafawa, ance idan ta shafa zata kara haske fatar nan tai jazur, wanchan Yar kam saisa nake tabbatar data wuni aikatau arana sabida ta dafe tai baki, bata isa ta kwacema y’ata farin jini ba, bebiya kawai” takarashe maganan tana zubawa Farrah dake tattare tukwanen

wajen harara, sanan tai wani irin murmushi tayi tana juya idanu, Malam dake kallonta kaman solobiyo yakara make murya yace “to adan zubo min” juyawa tayi tana murmushi tace “gobe ma ka karamin rashin kunya zanga mai baka abinci Malam” tawuce kitchen din ko kallon Farrah batayiba tadauki kwano a kwando tadeboma Malam shinkafar ranta nakara baci sabida yanda Farrah taci shinkafar sanan tarufe tukunyar tajuyo tace “kitashi kiwuce ki debo ruwa kicike kowani tulu na gidan nan inba hakaba nalahira saiya fiki jin dadi Al Qur’anin ubangiji” sanan tawuce takaima Malam abincin tazauna kusa dashi suna zance.

Ahankali tamike tsaye wani babban tulu tadauka tadaura aka sanan tafito daga kitchen din wani cinyayyen sidadden silipas wari daban daban tadauka a tsakar gidan tasaka sanan tawuce tafita daga gidan, daga Malam har Inna babu wanda yadagakai yakalleta.

Dasauri take tafiya abinta as usual dan sotake tagama cika ko’ina kafin mangariba tayi dan ba’a zuwa rafin idan Magrib yayi kuma rafin yamafi rafin wankinsu nisa, tayi tafiya mai tsawo kaman daga sama taji ankirata. “Ke Kurma” chak ta tsaya tana kalle kallen ko’ina babu kowa a hanyar, wani kalan murmushi tayi dayawani irin kawo cikakken annuri fuskanta cikeda kokarin son tai magana dan ga dukkan alamu tasan waye yakirata tace “taaaaaa…ffff….fa” wani irin dirkowa wata yarinya Yar matashiya tayi daga bishiyan mangwaro dake gefen hanyan da Farrah ke tsaye tana sanye da zani da riga na fulani kanta da dankwali baki na silk kana ganinsu kansu daya itada Farrah saidai tadanfi Farrah tsayi kadan itama farace sol kana ganinta kaga cikakkiyar yar fulani, wani kalan murmushi tayi takaraso gaban Farrah dake kallonta tamikamata mangwaro daya itama tarike dayan na hannunta tace “waike Kurman nan nace dole saikin kira sunana ne, barakije kiji da Kurmancin kiba iyye, sunana Shafa, ba Taaaa….ffff…..fa ba koyayama kike kiran sunan oho miki yar rainin wayau kawai” wani kalan murmushi Farrah tayi da saida ita kanta Shafa ta tsaya tana kallonta hakan yasa Farrah tahadiye murmushi da hannu tamata alamun me?, girgiza matakai Shafa tayi sanan ta tabe baki tasa hannunta daya takarbe tulun daga saman kanta tamaida nata kan tace “ni tausayi kike bani, muje naraka ki debo ruwan, rikemin mangwaro na nidai” tabata mangwaron dasauri takarba tana murmushi suka wuce, Shafa tace “Modibbo yakara tsareki a hanya”? Girgiza mata kai tayi dasauri alamun a’a, Shafa tace “yawwa, duk randa yakara tsareki karki nuna kina tsoronshi kawai kice yakiyayeki bakison matsalan su Rakiya, kindaisan yanda Rakiya keson Modibbo, ki kiyaye su” Gyadamata kai tayi alamun to tana murmushi duk kauyen nan Shafa kadai ce kawarta ita kadaice mai sonta, Shafa akwai baki kaman reza, gata da karfi tasha shiganma Farrah fada, har Rakiya tama duka akan Farrah dan ta tsani yanda ake wulakanta yarinyar sabida ita Kurma ce batada uwa da uba akauyen, son datake mata ne ma yasa bata taba kiranta da asalin sunanta Farrah saidai takirata da Kurma dan kowa yaji yes Kurman kauyensu ce kawarta. “Ke Kurma” Farrah taji ankirata dasauri takalli Shafa dataga tana kallon gabansu, ganin wasu maza su kusan shidda gaban rafin suna zazzaune sun zagaye murhu suna dafa shayi yasa Farrah ta tsaya

chak batare data kara tafiya ba kanta akasa, binsu da kallo itama Shafa tayi su Modibbo ne da abokanenshi suna dafa shayi gashinan farare dogaye kana ganinsu kaga yan fulani duk sun dago suna binsu da kallo suma, dauke kai Shafa tayi tajuyo takalli Farrah, hannunta tasa takama hannun Farrah tace “muje kinji Kurma” binta Farrah tayi gabanta nafaduwa dan ko hada hanya tayi da Modibbo bala’i yake zaman mata agida.

Wani dogon saurayi ne yatashi tsaye fari kal dashi kana ganinshi zakasan shine Modibbo sabida yanda yabi Farrah da kallo kaman yaga abinci, abincin ma gangariya, yana sanye da manyan kaya kal kal dasu babu datti dan Baban shi ne mai gari so sunada kudi gashi shine Magajin mai gari dan shi kadaine dan Maigari namiji, karasowa inda suke aduke gaban rafin yayi yana zuba hannu a aljihu yana kallon Farrah dabama taganshi ba ahankali yace “Farrah” dawani irin sauri daga Farrah har Shafa suka juyo suna kallonshi, hannun Farrah Shafa takama ta iza kan tulun dake cikin rafin tace “rike tulun nan Kurma” sanan tamike tsaye takalli Modibbo tace “Hamma Modibbo kaga bamasan bala’i kuma bama neman fitina karabu da Farrah dan Allah, nasan sabida ita ka kafa majalisa agaban rafin nan dan kasan tana zuwa debo ruwa, inhar kanason Kurma dagaske bazaka dinga jazamata bala’i ba bayan kasan Rakiya sonka take, kumama Hamma Modibbo waye zai barka ka auri Kurma iyye, dan Allah kafita harkan yarinyar nan ka tausaya mata, ka tausayama maraicinta haka mutanen kwarai suke” tunda take maganan yake binta da kallo saida tagama yanuna kanshi cikeda isgilanci yace “wai dani kike Shafa’atu?” Kwashewa da dariya abokanen sukayi ganin rainin wayon da Modibbo yama Shafa, daya daga cikin su yace “Modibbo bakin ciki take ba ita kakeso ba kawarta kakeso” wani mugun kallo Shafa tamai shikuma Modibbo yabi ta gefen Shafan yay inda Farrah take datake kokarin daukan tulun ta daya cika da ruwa zata iza bisa ka ganinshi yasa atsorace tasaki tulun zatai baya dasauri Modibbo yasa hannu yadauki tulun yarike yana kallonta yace “zona iza miki” girgizamai kai tayi ahankali kanta akasa taki zuwa, ahankali yataka zuwa gabanta yana kallon yanda jikinta kerawa sanan yadaura mata tulun aka dawani bala’in sauri kaman mazari tajuya zata wuce yace “bansallameki ba ai” chak ta tsaya batare data juyoba, hannunshi yatura a aljihu sanan yaciro ledan biscuit na Oreo dazun nan aka kawoma Mai gari biscut din daga binni nashine amman yakici dan yabata wani murmushi yakarayi yasan zata fara sonshi dan babu wanda yataba ganin irin biscuit din akauyen nan zuwa yayi tagabanta yamika mata ledan ta kalla sanan ta girgixamai kai ahankali yace “biscuit ne daga binni ki karba kona kama hannunki nasamiki” Shafa tadan kalla kaman zata fashe da kuka ganin haka yasa cikin fushi yace “idan Shafa kesaki tai abu kotahanaki kiyi abu zansa akoresu daga garin nan” akufule Shafa na tattauna baki tace “mafashi” dasauri Farrah tamikamai hannunta jin zaisa akori su Shafa, gently yasamata biscuit din yana murmushi sosai dasauri tawuce Shafa ma ta watsama dukansu harara tawuce shikuma yabita da kallo saida suka bace sanan yakoma inda suke ya zauna yana murmushi abokanenshi sukace “wai kai mezakayi da kurman nan ga hadaddun matan kauyen nan dake mutum maka kanace ma kurman nan mara galihu” wani kalan murmushi yayi yana karban shayin da aka zubamai a kopi kaman mai tunani yace “kap matan kauyen nan babu mai baiwar da kurman nan kedashi” Muji yace “wanan gajeran gata kurma wani baiwa tafi matan garin nan dashi Haba Modibbo Kodai magani tamaka ne” murmushi yayi sosai yadan

kurbi shayin sanan Ya hadiye yace “aradun Allah duka kauyen nan babu wanda yakai kurman nan kayan alatu ajiki, ahaka da wahalan da komi kaga kidirmon datake dashi kuwa balle ma nacigaba da bata dadi ina bata su kaza da biscuit’ din binni” yay dan dariya yana sake kurban shayi, tabe baki Muji yayi yace “kaima kasan kozaka mutu kanadai magajin gari baza’ataba barinka ka auri Kurman nan ba, babu wanda yasan ubanta, ance kanjamau yakashe uwarta ma, dataga tana shirin mutuwa ta tattaro da ita da yaran nata suka dawo nan kauye tazo tamutu anan” tabe baki Modibbo yayi yasake kurban shayin yajaye kofin daga bakinshi sanan yadagakai yakalli abokanan nashi daduk suke kallonshi suna jiran amsan shi dan dariya yayi yace “yo uban me kukeso nafadi muku? Kuda kunku kunsan ba aurenta zanba ai hakan yabaku amsan manufata akan kurman” wani kalan kwashewa dukansu sukayi da dariya suna tafi, Tanko yanunashi da yatsa yana kadakai yace “Modibbo, Modibbo anyi dan iska awajen nan wlh” suka kara kecewa da dariya, murmushi Modibbo yayi yace “gobe zaku kawomin ita dakina na gangare idan duhu yayi” tafi sukahau yi, Muji yace “kace kai Modibbo gobe Kwanan ango lahiya lau ne kaida Yar kurman ka” dariya Modibbo yayi yace “dasafe gobe zan kawo mata kwai da cinyan kaza da shayi, nabata dadi tabani kindirmo”.

Tofah jama’a ana wata gawata!
~Sai mun hadu mako nagaba dan jin yanda zata kaya tsakanin Modibbo da Farrah, shin Allah zai kubutar da ita daga hannun Magajin Maigari koko tana ruwa?? Kubiyoni danjin cigaban wanan kayataccen labarin na FARRAH wanda ni M Shakur ke kawo muku dahaka nace Bissalam😘~

💫FARRAH💫

✍🏻M Shakur

EPISODE2️⃣
Wani magidancin mutum ne da akalla zaikai 59 zuwa 60 haka aduniya yana sanye da suit dark blue yana sintiri cikin wani arnen hadaden falo yana kaikawo kana ganinshi kasan akwai abinda kedamunshi, daga gefen dakin kuma wajajen kofan shigowa falon wayansu bodyguards ne suna sanye da bakaken suit da bakaken glasses a idanunsu duk suna tsaye kikam kaman sojoji kagansu zaka dauka samudawane sabida girmansu dakuma karfinsu, wayan dake hannun daya daga cikin bodyguards dinne yahau ruri hakan yasa yadaga wayan yakalla sanan yadago kanshi yakalli mutumin dake sintiri a falo daidai shima mutumin dake sintirin afalo yakallo bodyguard din yace “Alhaji ne ko”? Cikeda girmamawa yace “yes sir” hannu yamikamai yana dan sauke ijiyan zuciya yace “give me the phone”? Dasauri yataho zuwa inda yake tsaye yabashi wayan karban wayan yayi yakai kunenshi yay shiru da alamu yana sauraron abinda

ake fadamai a dayan bangaren ne ajiyan zuciya yasauke yace “Yaya duk inda kace muje nan ne wajen shakatawan shi munje all of them bayanan, yanzu gamunan mun kara dawowa gidan shi, dukdai inda yaje dole agida zai kwana” shiru yasakeyi sai chan yace “eh achan bayan layin ma mukai parking, bazaima gane akwai mutane agidan ba Yaya, karka damu zamu dawo maka da Zayn Yaya, I promise I will not disappoint you” dan murmushi yayi sanan yazare wayan daga kunnenshi yabama bodyguard din sanan yajuya yadaura hannayenshi kan saman kujeran dayake tsaye gefenta yasake sauke ijiyan zuciya daga gani kasan akwai abinda kedamun shi sanan ahankali yakara mikewa tsaye yana gyara zaman agogon hannunshi this is 3:27PM, tun wuraren 8 suka duro garin nan amman basugan yaron nan ba, kaman daga sama sukaji karan gate na budewa dasauri yay wajen window dakin yanasa hannu a lips nashi yana kallon bodyguards din alamun kar wanda yay magana sanan kaman barawo yadan dage gefen labulen window kadan yana kallon tsakar gidan, dayake remote gate ne budewa katafaren gate din yayi da kanshi wata arniyan Ferrari 296 GTB ce ta danno kai cikin gidan wani irin ijiyan zuciya mutumin dake leken yasauke yace “there we go, Alhamdulillah, Allah ya jefoka finally Yaya zai barni nasha ruwa da kyau” yakara gyara tsayuwa yana leken kaman barawo, kashe motan akayi amman ba’a fitoba, girgiza kai mutumin dake leke window yayi yace “malalaci nasan gajiya yayi yanzu haka hutawa yake” yana nan yana kallon motan kusan 10min sanan aka bude kofar motar, damn! What a ride! Wato Kofar motan sama yayi da aka bude, ahankali kaman ba’aso ayi wata black beauty leg dake sanye cikin wani brown Tomford Wicklow logo suede sandals yafito, kumbunan kafan nan farare sol kaman ana gyarasu da chalk and milk tsabagen kyansu, kafafun saida sukai kusan 1min awaje sanan ahankali wani dogon cikakken lafiyayyen matashi yafito daga cikin motan yana bama window baya yana maida kofan motan yana rufewa, wani off white jacquemus Le Gelati bermuda short ne ajikinshi daya tsayamai iya guiwa, yahadata dawata AMI Paris coeur hoodie brown akai, kana ganin kayan dake jikinshi from leg to head designers ne, juyowa yayi ahankali yanadan yatsine fuska sabida ranan daya hasko fuskanshi bakinshi na tauna cingam, wani kyakkywan black beauty guy ne dakeda wasu irin jajayen lips, yanada manyan idanu dakuma dogon hanci, gashin kanshi a kwance gashin sajenshi suna shinning saidan gemun dayadan tara wanda kana kallon gemun zakasan na yan iska ne dan gefe daya baki gefe daya fari yayi dying rabin gemun, yanada cikan jiki dan full guy ne baida rama ko kadan kaganshi zaka dauka all this black American rappers ne, fuskanshi yadan shafa zuwa gemunshi dayadan ja sanan yasake yatsine fuska yafara tafiya ahankali kaman baiso yayi zuwa katafaren only flat dake durmemen gidan dakenan da Glassdoor, yana kaiwa gaban Glassdoor din password dinshi yasa sanan ahankali yatura kofan yashiga ciki chak ya tsaya yanabin mutanen dake dakin da kallo one after the other kafin idanunshi yasauka kan mutumin dake tsaye wajen window daya juyo yana kallonshi murmushi kan fuskanshi, daure fuska yayi tamau kaman baisan menene murmushi aduniya ba sanan yawuce ciki yana tafiyan nan agajiyance yacigaba da taunan cingam dinshi yay hanyar dinning, dasauri magidancin mutumin yabishi yace “Zayn yanzu Uncle dinka baida darajan gaisuwa ma a wajenka”? Kaman badashi ake magana ba kojuyowa baiyiba yakai gaban lafiyayen fridge din dake dinning mai kama da madubi, hannunshi yasa yabude fridge din yasa hannunshi zai ciro bottle water cikin wata kalan lazy voice yace “what do you want Uncle”? Yay maganan yana bude marfin goran ruwan ya tofar da cingum din bakinshi anan kasa yakafa ruwan abaki yana sha, kallonshi mutumin daya kira da Uncle yakeyi  kaman yaga abin kallo saida yaga ya shanye ruwan tass ya

jefar da goran da marfin duka akasa kaman wajen bola ne, goran dasu cingum din daduk yazubar akasa ne Uncle din yabi da kallo sanan yakalleshi yace “Zayn Baban ka yace nazo nataho dakai Nigeria” Dawani irin sauri yakalli Uncle din nashi fuskanshi karara yanuna bacin rai, dauke kai yayi yajuya azuciye yafice daga dinning din yace “I am not going anywhere Uncle ka kwashe yaran nan daka kawo kubarmin gida” yayi hanyar kofa zai fita da idanu Uncle yama bodyguards din alamu su tare kofa hakan yasa sukai wajen suka tare kofan dukansu su 6 din, chak ya tsaya yana kallonsu ranshi a bala’in bace hakan yasa cikeda bacin rai yawani irin juyo yakalli Uncle din nashi yanamai kallon what is all this, anatse Uncle din yace “it’s an order Zayn daga mahaifinka, bazamu taba barin garin nan ba saida kai, so get parking mu wuce” runtse idanunshi yayi da karfi sabida takaici, yanda ranshi ke tafarfasa azuciye yayi wani irin ball da flower verse din dake kan center table na falon wanda akalla kudinshi zaiyi 5Million, jikake rukukuuuu karan fashewa sanan awani irin wuce zuciye yafada kan lumtsatsen kujeran falon ya zauna jikinshi na bari sabida fushin dayake hannunshi na rawa yatura cikin aljihun hoodie dinshi wani hadaden kwali yaciro na Doubletree cigarette kaga kwalin bazaka taba sanin taba bane zaka dauka wani chocolate ne ashe taba ma akwai na yan gayu, kara daya ya zaro sanan yadauki wani very cute lighter dagakan centre table dinshi ya kunna taban yazuka yana fuzar da hayakin sanan yadauki wayanshi wani custom made iPhone 13 ne da akayishi da gold yay dialing number dayay saving da Papa, ringing daya aka daga kaman jira yake yamike tsaye cikin fushi sosai still karan taban na hannunshi yace “what is the meaning of all this Papa? Are u baby sitting me now ne or what exactly? Am I a kid nizaka aika a dauko maka tundaga Nigeria harnan Indianapolis, am I some toy to you ko ina crèche dazaka wani aika a daukoni huuun Papa”? yay maganan yana jefar da karan taban hannunshi dan bayama barinshi yay masifa da kyau, da sauri Uncle yakaraso yatake taban yana murjeta da takalmin shi kafin yaja gobara agidan, sanan yakoma inda yake tsaye yana kallon Zayn din da wayan ke kunnenshi ko kaffara bazaiyiba idan ya rantse yasan lallashinshi Yaya keyi, kaga yanda yakema mahaifinshi masifa zaka dauka dawani mate dinshi yake magana, sunkai kusan 20min suna wayan sanan yakalli Uncle din nashi ranshi abace yawani jefar da wayan tashi awulakance akasa Uncle din yabi wayan da kallo sanan kawai ya girgiza kai yaduka yadauki wayan yanabin wayan da kallo dahar ta tsage sabida yanda yajefarda ita sanan yakai wayan kunnenshi yana sauraron abinda Yayan shi kefadamai, cikeda girmamawa yace “to Yaya, In sha Allah Yaya, yanzu zamu taho Yaya, tom I promise” ya katse wayan kafin ahankali ya ijiye wayan kan kujeran kusa da Zayn din dake huci sanan yawuce stairs, wani daki yabude dazaka dauka dakin governor ne, komi a gyare akwati daya yadauko yashiga hadamai kaya wanda yasan kawai wahalar da kanshi yake dan kawai afaranta mai raine Yaya yasashi Wanan aikin dan basaka kayan zaiyiba, tass yahada kayan sanan yadauko wani Versace bargo mai bala’in laushi yarike a hannunshi yafito yakira wani bodyguard yazo yakarba yafice dashi tsakar gida wani yabiyoshi sukaje suka kwaso motocin dasukai parking chan zuwa gida aka jera komi a mota sanan suka dawo, Uncle yadubi Zayn din dake zaune inda yake akan kujeran ya kishingida da kujera ya lumshe ido yace “let’s go Zayn everything is set” dan bude idanunshi kadan yayi yakalli Uncle din nashi sanan yace “I need 5min nap” wani irin ijiyan zuciya Uncle Hali yasauke yana kallonshi kawai irin kallon nan na babu yanda ka iya da mutum, yana tsaye akanshi saida 5min din yacika daidai sanan yace “Zayn 5min yayi tashi muje dare nayi” ko motsi baiyiba kuma Sarai yasan yana jinshi hakan yasa yakalli bodyguards din yace “kuzo ku dauke shi” bude idanuwanshi yayi da sauri yamusu

wani mugun kallo sanan azuciye yamike tsaye yace “duk wanda keson rasa aikin shi yau yazo yatabani yagani” sanan yawuce yafice daga dakin rai abace bodyguards din suka bishi abaya dasauri, Uncle kuma ya tsaya yakashe komi na gidan sanan yafito rikeda wani bagpack na yan tarkacen abubuwan Zayn din ya kulle dakin yawuce wani babban jeep da yasan nanne Zayn din yake ciki bodyguard yabudemai kofa yashiga yazauna kusada shi, dauke kai Zayn yayi yana kallon hanya ko kadan baiso Wanan tafiyan ba babu yanda zaiyi ne kawai he’s so hurt, cikin wani irin fushi da neman bala’i yace “where is my headphone Uncle” da sauri Uncle din yashiga bude bagpack din yace “gashinan na dauko maka cus nasan you will ask for it” yay maganan yana cirowa yana mikamai, wani irin fizgewa yayi daga hannunshi sanan yadauke kai cikin kunkuni yace “I hate this old man” sarai Uncle yajishi murmushi kawai yayi yana girgiza kai irin na manya yaciro wayanshi yana daddannawa, ahaka sukakai airport bangaren PJ, budemusu motan akayi, Zayn yafara sauka daidai da wayanshi bai dauka ba yabar shi kan kujeran duk Uncle na lura yasan neman abinda zai hanasu tafiyan nan yake at all cost kuma hakan bazai taba faruwa bane, dakanshi ya tattaremai wayan da komi nashi sanan yafito daga motan bodyguard din suka rufe suka wuce wajen jirgin Zayn shi harya shige, shiga Uncle yayi yaganshi zaune kan 3sitter chair jirgin ya kishingida ya lumshe idanu kaman mai bacci dake komawa gado, bargonshi Uncle yakarba daga hannun bodyguard din yazo wajen ya ijiyemai a gefenshi, sanan ya ijiyemai jakan tarkacen shi, saida suka gama komi sanan 4 daga cikin bodyguards din sukama Uncle sallama suka wuce, shikuma uncle da 2bodygurads din suka nemi waje suka zazzauna kowa yasa sitbelt nashi, wata Moroccan air hostess ce tafito cikin turencin ta na Arabs ta gaida su Uncle sanan takalli Zayn dakenan kaman yau bacci tace “Sir is sleeping, I think we ready” sanan tajuya dan kullo kofa Zayn yadan bude idanunshi kadan yanabin bombom dinta da kallo dan short skirt tasaka sanan yadan yatsine fuska ya bude idanunshi tass yakalli Uncle cikin fushi yace “where is my phone? Kuma am hungry” anatse Uncle yace “ga wayanka nan ajakan dake kusada kai, abinci we are about to take off, let’s take off saikaci ko” daure fuska yayi yakalli jakan bazaima iya budewa yadauki wayan ba, hakan yasa Uncle yacema bodyguard din “give him his phone” tashi yayi yazo yabude jakan yadauki wayan yabashi karba yayi yace “with the headphone” ciro headphone din yayi yabashi ya karba yana makalawa a kunnenshi shikuma bodyguard din ya maida jakan yarufe sanan yatashi yakoma wajen zamanshi, air hostess din ta rufo kofan jirgin sanan tadawo ta zauna akan kujeranta dake facing mutanen jirgin tana kallon Zayn dake tabe taben wayanshi tanadan murmushi takasa daina kallon handsome black Nigerian richboy din dakowa na jirgin nan uban yaron yakema aiki hatta pilot dinsu dan jirgin nan daya daga cikin jiragen Baban shi ne, she has been hearing labarai daban daban kan only don din boss dinsu kan bayaji menene menene but bata taba sani he’s this cute, sexy and handsome ba, jibi yanda yake abinda yaso kuma dole abishi wayan nan ma bayanda ya iya ne shima hala da cewa zaiyi arikemai yay ta tabawa tasake sakin murmushi.

Jidayayi ajikinshi ana kallonshi yasa ahankali yadago idanunshi karaf idanunsu sukai clocking awani irin kunyace ganin yakamata tahau murmushi tana shafa kanta, dan tabe baki yayi irin na yan iskan yaran nan sanan yawani kashe mata idanu daya yakai hannunshi yaja dan iskan gemunshi dinan idanunshi kan fararen cinyanta, jitayi kaman zuciyanta zai buga ganin yanda

yake kallonta da mayun idanunshi tahau murmushi tana kokarin dauke kai takasa, Uncle dinshi yakalla ganin yafara bacci daga gani kasan yagaji tun safe halan yasan suka shigo garin nan suna nemanshi ko tausayinshi baijiba ya kwalamai kira. "Uncle Uncle" firgigit Uncle yabude idanunshi yakalleshi yace "Zayn mekakeso" "food" yafadi atakaice dasauri Uncle yakalli air hostess din dahar tafara cire sitbelt zata tashi tace "I am on it sir" sanan tawuce da sauri tai kasa zuwa kitchen Zayn yabita da kallo ta gefen idanu, lafiyayyen abinci takawomai a tray da wine tazo gabanshi tana murmushi still tashiga ijiyewa yana bin ko'ina najikinta da kallo saida tagama sanan takalleshi cikin idanu tace "enjoy your meal sir" dan lunshe idanu yayi yabude su saida kirjinta yabuga what! This guy is super hot Innalillahi zuciyanta yagama narkewa akanshi, sanan tawuce wajenta ta zauna tana saka sit belt Uncle kuma yakoma bacci dan ya bala'in gaji, sosai take kallonshi yanda yake tsatsakuran abinci yaci Wanan ya yatsine fuska yature yaci wanan karshe non alcoholic wine dinne kawai yadansha sosai in a very lazy voice yakallleta yace "take it away" gyadamai kai tayi ta taso dasauri tazo ta shiga kwashw komi tana lumshe idanu kamahin dayakeyi na neman tafiya da ita sanan tawuce takai komi ta ijiye tadawo tasake zama wajenta tana kallon shi, dan tsaki Zayn yayi sannan yadan kalli Uncle ganin bacci yamai dadi harya farajan minshari yasa ahankali yacire belt yatashi ko kallon bodyguard din baiyiba yawuce kasa yarinyar na binshi da kallo, hannunshi yatura a aljihu yaciro kwalin taba duk tana kallonshi sanan yabude bayin jirgin yashiga yasauke marfin clean masan bayin ya zauna ya kunna taban yashiga sha Ahankali yace "I hate planes" knocking kofan dayaji anyi yasa akufule yace "who" ahankali tace "is Marie sir, smoking on board is not allowed sir" tai maganan ahankali, bude kofan bayin akayi taban na bakinshi yawani kalleta daga sama har kasa sanan yazare taban daga bakinshi yabusa mata hayakin a fuska yace "are you going to fine me for smoking or what?" Wani kalan murmushi tayi yanda yamata maganan saida zuciyanta ya narke, da yatsu yamata alamun tazo, dasauri ta shigo cikin bayin maida kofan yayi yarufe sanan yawani irin mannata jikin kofan yana sake busa mata hayakin a fuska yace "you seems to want me badly huh?" Jitayi kaman numfashinta zai dauke kirjinta na faduwa fat fat, anatse yace "how much is your pay" ahankali tace "8000 pounds Sir" cillar da karan taban daya gama sha yayi a wash hand basin sanan yadaura hannunshi gaban riganta yana bude mata boturin rigan yace "I will pay you x5" yay maganan daidai yagama bude boturan da boobs dinta matsakaita suka bayyana tabe baki yasakeyi yace "not bad" sanan yakai hannunwanshi duka biyun yawani damke su da karfi, wani irin malalacin kara tasaki tace "auuuch Sir, what are you doing, we are on plane let's land first is not allowed, having sex on plane is risky" wani irin juyarda ita yayi yana daura hannuwanta kan wash hand basin din yana kwaye skirt dinta sama yace "I guess I love risk" yawani kalan barka pant dinta gefe sanan yashiga bude gaban wandonshi, kiris yarage bata Kurma uban ihu ba tashayin sex but yau kalan abinda yashigeta bata tabajinshi aduniya ba no wonder akace African men barinma Nigerian men are monsters, God takes his time in creating their dicks well, this rich handsome dude here is not a human, he fucked her good sanan yawani irin hankadeta gefe anan wash hand basin din yakawo tsaki yayi duk Papa yajamai yana fucking wata air hostess she's not even sweet, maida Hajiyar yayi cikin wandonshi sanan yawuce yafita dudda Joystick din bai gama kwanciya ba ko kallonta bai karayi ba, hada idanu yayi da Uncle dake binshi da kallo ko yaushe yatashi ohon mishi, shafa gemunshi yayi yana yatsine fuska ko ajikinshi sanan yazo yay kwanciyanshi kan kujeran batare daya kalli Uncle dinba yace "I want to sleep uncle alullube ni" ajiyan zuciya kawai Uncle yasauke sanan

yakalli bodyguard din da idanu hakan yasa yatashi yadauki bargon ya rufamai ko cikakken 5min bai daukaba bacci yay awon gabadashi.
Takai kusan 10min zaune akasan bayin sanan ta lallaba ta tashi tana kallon kanta a madubi yan fararen nonon ta harsunyi ja sabida yanda yadinga matsesu da hannunshi danko kadan baisha ba, bra daya cillar akasa tadauka ta maida sanan tasaka rigan tai fitsari sanan ta tashi ta gyara kanta tsaf tsaf tana mamakin karfin shi dole yammata su dinga kuka suna rokon yaron nan yay dating nasu, ahankali kaman barauniya tabude kofan bayin tafito kanta akasa Uncle yadauke kai kallo daya yamata yariga yagane komi skirt dinta dukya yamutse kawai ya girgiza kai, at this point Zayn kawai sai Allah ya shirya, yaro baya tsoron uban kowa Allah ka shirya yaron nan.

Yanada bala'in nauyi dakuma sound sleep, idan yana bacci bacci yake kaman dan shugaban kasa harsukakai Nigeria baisan sunkai ba, parking jirginsu yayi a babban airport na birnin tarayya Abuja, Baban shi Tajudeen Ganuwa shine the second richest person world wide, yanada jirage Ganuwa airlines, international da domestic flight, sanan yanada PJs wato private jets dakuma choppers su helicopters dan har gwamnati na hayan jiragenshi, banda haka business nashi is mainly kan natural resources na Nigeria, cementi, tiles, mai da gas, kayayyakin abinci, da transportation kuma, matayensu hudu amman Allah baitaba bashi haihuwa ba sai akan Zayn wanda he's just 26yrs old yanzu amman idan kaganshi sabida girman jiki dakuma tsayi daya dauko na mahaifinshi zaka dauka yakai talatin kokuma yay irin su 35haka ko 38 nan ko he's just 26yrs old.
Ma'aikatan Baban shi suka hadu aka hada wani bouquet na welcoming yaron Boss dakowa kejin labarin shi amman baa taba ganinshi ba dan a Turai yake zama,
saida bodyguards din suka gama fitada komi sanan Uncle Hali yaje kanshi bubbuga kujeran yayi yana kiran sunanshi ahankali. "Zayn! Zayn, Zayn" dan bude idanunshi kadan yayi yadaurasu akan Uncle idanun sunyi ja alamun mutum yasha bacci sosai kafin ahankali yatashi zaune yana yatsine fuska murya chan kasa yace "Uncle water" dasauri Uncle Hali yashiga waigawa ganin air hostess din a tsaye wajen gaban cockpit yasa yace "I want water" dasauri tace "yes sir" bottle water takawo Awani tray mai kyau da karamin glass cup takawo tana kallon Zayn din dabaima san ko akwai wani mutum awajen ba, karban ruwan Uncle yayi yazubamai a cup yabashi yasha tass sanan yamike tsaye ahankali dasauri Uncle yasa hannu yakwashe blanket din daga jikinshi dan ya yaye blanket dinma bazai iya dakanshi ba sanan yawuce yafara tafiya ahankali agajiye batare daya juyoba yace "Uncle pay that girl up" dudda yarinyar bayar naija bace irinsu basusan kunya ba amman saida taji wani irin mugun kunya kaman ta nitse akasa, yanda yay maganan abiyata kaman wata mara daraja shi kanshi Uncle kasa kallonta yayi dan bazai iya Wanan lalatan da rashin kunyan yaran zamani ba besides ma yarinyar ma'aikaciyar suce, hannu kawai yasa a aljihu dollars ne ajikinshi duka bandir bandur na dollars din kawai yaciro ya zubasu akan kujera sanan yawuce yafice itakuma ahankali tadaga kanta tana kallon Zayn din ta window first class playboy ne Zayn, irin no string attach sex dinan yake da mata, kudin takalla data samu saikuma tai murmushi this is salary nata na kusan 8months tattare kudaden tayi dasauri sanan tawuce ciki abinta.

Wasu kalan layi manya manyan motoci sukayi ga bodyguards rututu awajen, direct Uncle wajen wata BMW M3 Touring car yayi baka dan yasan nan ne Zayn yake ciki yana zaune daddanna waya yake abinshi haryasaka cingam abaki yana taunawa yanadan murmushi shi kadai yana kallon wayan, rufe kofan akayi sanan aka jasu.

Wani anguwa suka shigo wanda tundaga bakin titi harzuwa karshen anguwan gidansu ne, gate na gidan guda 7 ne in total, yatsine fuska yayi dasuka shigo gidan murya chan kasa yace “I hate this house” gidan ina gani ko gidan shugaban kasan Nigeria bazai nunama gidan kyau ba, different security check post, cameras takowani angle da bangare, electric fence, finally suka karaso cikin katafaren asalin gidan dazaka dauka gida ne da aka gina wajen beach haka a Florida dan vibe din Florida gidan ke bayarwa, komi na gidan is glass,  ga ma’aikata kowa na sintiri yana kaye kaye, wani magidanci mutum ne yafito yana sanye da manyan kaya farare fat yana zuba uban kamshi yana tafiya da gudu gudu sauri sauri yanama su Uncle alamu karsu magana, kana ganinshi kaga Zayn kaman yayi kaki ya tofar, he looks very feet kaman baikai 40yrs ba nan ko he’s 65, yanada kyan jiki bana wasa ba kuma tsabagen kudi ne dacin abincin daya dace, idanunshi kadai zaka kalla zaka gane irin tsantsan son dayake ma Zayn sabida yanda yake kallon Zayn din dake fitowa daga mota yana danna waya danko lurada shi baiyiba, yana zuwa wajen baiyi wata wata ba wani irin rungume Zayn yayi tsamtsam ajikinshi yana sauke ajiyan zuciya, anatse cikin murya irin na manya yace “Alhamdulillah, Alhamdulillah, Allah nagode maka daka iso da d’ana gareni lafiya, Ya Allah nagode maka, zanyi azumi guda uku just to thank you more Ya Allah daka dawomin da Zayn lami lafiya” wani irin yatsine fuska Zayn din yayi yana juya idanu irin na if u are done ni kasaken, ahankali mahaifin nashi yasake shi yana kallonshi sanan yakai hannunshi yakama habanshi yana kallonshi yace “Maiya sameka karame bakacin abinci ne come here” yamanna mai peck a goshi, daure fuska yayi yace “where is Ummi”? Murmushi Baban nashi yayi dan yasan fushi yake dashi saisa yaki kulashi yace “muje Maman ka naciki tamaka favorite abincin ka, she cannot wait to see you”.

This is last free page, payment is 500 into 3107021073 aisha Muhammad first bank
Chat me up directly
wa.me/+2347012181461

💫 FARRAH 💫

✍🏻M Shakur

EPISODE 3️⃣
Fizge hannunshi yayi daga hannun Baban nashi yawuce ciki yana tafiya kaman bayaso yayi agadarance Papa yajuya yabishi da kallo kaman baitaba ganin shi aduniya ba. “Yaya” Uncle yakirashi anatse dayasa firgigit yajuyo dasauri yana murmushi yace “kaga yanda Zayn ke kara girma kullum yamafini tsayi fa” dan murmushi Uncle yayi yace “ai tun Zayn na yaro yakeda saurin girma, babu wanda zai ganshi yanzu yabashi asalin shekarun shi 26 saidai adinga bashi 30 sama” sosai Papa yashiga dariya irinta manya yana kara leken Zayn din daya bace musu daga gani, sanan yajuyo yakalli Uncle yace “dan kanina ya akayi”? Yay maganan yana kama hannunshi cikeda so, murmushi Uncle yayi yace “zan wuce gida naje nai wanka nadan kwanta Yaya” cikeda so dakuma damuwa Papa yakai hannunshi kan shoulder nashi yace “you must be extremely tired ai dole ne, stress na Zayn is energy draining, kaje kai wanka kahuta I will see u anjima da daddare kokuma dasafe just take your time kaji idan zakazo ka taho da su Rukayya da yaran suzo su gaida da dan uwansu” gyadamai kai yayi ahankali yana murmushi yace “to Yaya bari naje” gyadamai kai Papa yayi yana sakinshi yace “u can dismiss wayan nan guards suma suje suhuta I will see you later okay” yay maganan Papa yawuce ciki.

Wani gagaruman falo Zayn yashiga yana tafiya kaman bayaso yayi ma’aikatan gidan tundaga nan compound ke zubewa suna gaidashi kaman anga Sarki ko kallonsu bayayi yashige falon abinshi, wata babban mata gatanan fara fat ke tsaye agaban dinning, tana sanye da wani arnen lace dayasha aiki mai suna aiki, idanunta sanye da fararen glasses kar wanda kana ganinsu kasan na kara karfin idanu ne, tana tsaye inda take tanama yan aikin pointing komi da yatsunta dasuka sha jan lalle tana nunamus yanda zasu jera abinci dakenan cikin lafiyayyun kuloli ubansu dakake gani a irin gidajen sarakunan larabawa tabama kofan baya hakan yasa ko kadan bataji shigowan Zayn dinba, kotaji ajikinta ana kallonta ne chak ta tsayar da maganan datakeyi da ma’aikatan sanan ahankali tajuyo kaman wanda wani abu yakirata, chak ta tsaya tana kallon Zayn dashima kallonta yake yana dan murmushi, ance uwa uwace kuma koyaya take dadi ne da ita, ahankali takai hannuwanta ta rungume su a kirji tai jim tana kallonshi daga sama zuwa kasa kaman mai tunanin wani abu tama kasa koda motsi daga inda take tsaye, wani kalan murmushi Zayn yayi dan yasan metake kallo sanan yataho da sauri har zuwa gaban dinning din ya tsaya agabanta yana kallonta yana murmushi ganin yanda tayi yasan fada zatamai hakan yasa kawai yakai hannuwanshi yajawo hannunta dagudu, ware ido tayi tace “mehaka Zayn? Mehaka kake jana”? Saida suka kawo tsakiyan falon sanan ya tsaya yakama dayan hannunta yarike yafara juyata yace “we are dancing Ummi, Ummi I am now taller than you sosai” yanda yashiga juyata yasa idanunta suka fara kadawa dasauri ta fizge kanta tana tangan tangan ta dafa kanta tace “jama’a na shiga uku, sabida kahadiyi kadan jimina kafini tsayi yanzu shine yabaka right kamin juwa juwa” dasauri tazauna akan kujera tana maida ijiyan zuciya, dariya yayi sosai yana kallonta kaman bashine ke kumbure kumbure awaje ba yazo kan kujeran datake yawani kwanta yadaura kanshi kan cinyanta sanan yakama hannuwanta yakai

kan fuskanshi yana sauke ijiyan zuciya yace “massage my face Ummi nagaji” yay maganan yana lumshe idanu ahankali tafara massaging face nashi tana kallon gemunshi dayama kala sanan anatse takai hannunta kan gemun takama tarike tana kara tabbatar da kala ne wato tura gemun yayi murya chan kasa tace “Zayn wanan kalan dakama gemunka na menene”? Dan yatsine fuska yayi batare daya bude idanunshi ba yace “Ummi is fashion, bakiga Kenye west ba haka nashi yake” dan jim Ummi tayi sanan tace “Zayn menene abin burgewa anan amatsayinka na dan musulmi, annabi yace duk wanda yaso wasu kokuma yayi koyi dasu to ranan tashin alkiyama tare Za’a tashesu yana cikinsu, waye kuma Kanye west? Zayn haka mukai dakai? Bakamin alkawari zaka dawo yaro mai tsoron Allah ba dakuma koyi da sunnar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata agareshi, yanzu when was the last time kadauki Al Qur’ani ka karanta”? Minshari yawani jaaa irin baimasan tanayi ba dinnan kuma tasan sarai yana jinta, ahankali tace “Zayn ina maka magana kana minshar…..” “Why on earth are you disturbing my son Doctor? Daga dawowan shi” sukaji muryan Papa daya shigo dakin afusace hakan yasa tadago kanta dasauri takalli Papa zatai magana yadaga mata hannu alamun tai shiru yakalli Zayn din daya lumshe idanu yace “yaci abinci”? Girgixamai kai Ummi tayi, sosai fa cikeda masifa Papa yace “akan wani dalili zaki tasamin d’a agaba kina damunshi batare dakin ma bashi abinci yaci ba eh Doctor? Kinsan awa nawa yayi cikin jirgi nifa idan bakison yaron nan ni inason d’ana, nakuma san darajan shi, nasan me Zayn yamin, yaron nan yazame mini sila na farin ciki dakuma karin yalwan arziki dan haka kisan yanda zaki dingama d’ana magana, kome yakeso kibarshi yayi yaro ne he’s just 26, nan gaba koda kudi, bama kudi ba kodame zaki hadashi kice yayi shiga haka ko dressing haka wlh bazai yiba komi dakike gani na duniyan nan lokaci ne, Zayn” yakaraso wajen yana bambami yadago kanshi daga jikin Ummin dake kallon Alhaji turus kawai kana ganinta kasan batada tacewa, ahankali Zayn yatashi zaune yana dan bude idanunshi yana kallon Alhaji, dasauri Alhaji ya tallabi fuskanshi yace “kyale Maman ka tacika fitina, ni nasan sabida itane yasa bakasan dawowa Nigeria dan tasamin kai agaba take, yanzu ko zan tsaya tsakin daka babu wacce ta isa tadameka wlh, muje

Ganin haka yasa Farrah tafito daga inda take leke dan ita tazagayo tabaya ne tazo gaban Zayn da shanu ya kare da guduntа, baima lurada ita ba ko kadan sabida wahalan dayake ciki hannun mutum kawai yaji an daura akan kafadarshi daga tabayanshi dayaji wani kalan sanyi ya shigeshi saikace hannun kankara dasauri yadago kanshi da idonshi kwara daya dayake iya kallon mutane dashi daya kankance Ya daurashi kan Farrah, cute little farin index finger dinta Farrah tadaura kan pink lips dinta alamun yay shiru, bama ta tsaya kallonshi ba tasa hannunta da bala’in sauri tashiga warware mai kullin da akayi a hannunshi Zayn nawani irin kallonta da ido daya tazare igiyan hannun ta yar, sanan tashiga kwance na kafan nashi da bala’in sauri kafin kidnappers din su juyo suganta, tundaga kan hulan kiwon dake kanta yake kallo irin na kauyen nan da akeyi da itace daya daure igiyan akasan gemunta yake kallo, zuwa gefen fuskanta da gashi ke kwance akai kaman na yar jaririya har zuwa kumatunta zuwa red dogon bead Earings dinta dake lilo a kunnenta zuwa fararen hannuwanta datake kwancemai igiyan dasu, kodan yana tsakiyan azaba ne and she appeared from nowhere but ahankali cikin muryan dashi kadai zai iya jinta yace “is she an angel?” Wani kalan fincikota akayi. “Ke Yar Fulani? Dama Kece kika cika mana wajen nan da tumakai”? Oga daya damki Farrah yafadi hankali tashe ranshi abace.

To jama’a is FARRAH going to be okay???

💫 FARRAH 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 🔟

Damke wuyan Farrah yayi ganin sotake ta taimaki wannan yaron da sukeda burin samin duniya ta sanadin sa, wani kalan jijjigata yayi yace “kinsan wanene kike shirin kwancewa ke agwai?

Kinsan biliyan nawa zamu samu akan yaron chan”? Ihu Farrah tayi da kyar danji tayi kaman zata shide sabida yanda ya damke wuyanta, kokawa tashigayi tana kokarin kwace kanta amman takasa kwace kanta daga hannunshi sabida karfin dayake dashi, Zayn ta kalla da kidnappers biyu suke tsaye kanshi dayan nakokarin daukan igiyan yasake daureshi, bin dan jinin dagefen idanunshi ke fitarwa tayi dakuma karyayyen hannunshi taji wani kalan karfi da kwazo yazomata bazata bari su kashe yaron nan ba, maybe yanada iyaye yanada kannai dazasuyi tunaninshi kaman yanda kusan kullum take tunanin Yar uwanta da aka kashe agabanta, wani kalan ihu Farrah ta yanka. “Eeeeeeeeeeeeee!” Shi kanshi Oga baisan lokacin daya saketa ba yay baya yana kokarin taushe kunnenshi dan muryanta yay wani kalan piercing dodon kunnenshi, dawani kalan sauri cikin bala’in kwazo da jarumta da ita kanta batasan tanada shi ba tajuya batai wata wata tai kan Oga dake karkade kunnenshi sabida yanda yakejin ihunta har yanzu, gabanshi tasha hakan yadago kanshi zai kalleta tai targeting kwayar idanunshi goran yajin ta danna ta fesama a fuskanshi da bala’in yawa, Ya shiga idanunshi da kyau ya shiga hancinshi atake yashaka da baki, ihun dababu shiri Oga yayi yajuya ahaukace gabaki daya yama zare danjin yajin yayi har kwakwalwa yana tattaba fuskanshi azare yace “ku kamata Lamba takasheni da yaji, wayyo idanuna” juyowa tayi da sauri jin yakira mata sauran, Lamba da dayan sukayo kanta, daganan inda take ta fesa musu dudda suna kokarin kaucewa amman saida ya shiga kwayar idanunsu da jikinsu dan har fatan wuyansu ta watsamawa sukahau ihu suma kowa yay gefe azare wato yaji bala’i ne barinma awajen maza, ganin haka yasa ta arto aguje inda Zayn yake yana kallonta kaman wanda har yanzu bai yarda cewa mutum bace, da duka karfinta takai hannuwanta takama hannunshi mai lafiyan tana ihun kokarin magana with so much force. “Ahhhhh jeh….jeh..…” tana kokarin gayamai suje da baki da hannu, da kyar Zayn ya iya tashi yana kallon yanda hannunshi ke lilo kaman ba hannunshi ba, sakin hannunshi mai lafiyan Farrah tayi tazo ta bangaren hannunshi mara lafiyan ahankali takama hannun saida Zayn ya lumshe idanu hawaye suka zubo sharrrr, daura hannun tayi akan kafadarta sanan takai hannunta daya kan waist dinshi dan yafita tsayi sosai tafara tafiya dasauri dasauri tana waigen bayan su, Oga dasu Lamba na kasa suna fama da yaji kaman wayanda jinnu yabuge, Lamido dasai yanzu ya iya tashi daga wurgan dashi da saniya tayine yashiga gyara bindigarshi da settings din ya birkice sabida barar dasu da akayi, ganin zai harbesu yasa Farrah tawani ja Zayn dawani kalan gudu shima Zayn dayaga bindiga wani kalan karfin gudu ne yaji yazo mai sukahau gudu kaman ba gobe, harbi Lamido yafara yana binsu dagudu shima cikin ikon Allah ko bullet daya bai samesu ba sabida yanda suke famfala gudu, sosai Zayn ke gudu yana kallon gefen fuskan Farrah da kusan itace jagoran gudun nasu tana zufa sosai, dan nauyin hannunshi na kanta, baitaba ganin brave yarinya karama kaman itaba tunda yake in his life, shi baimasan mata can be this brave ba sai dai a tv!

Juyawa baya Farrah tayi dan hakanan jikinta yabata wani abu, wani katon dutse Lamido ya dauka yawani jefo musu yayo saitin Zayn, cikin zafin nama tasaki hannun Zayn karyayye sanan tawani fada kirjinshi ta kankame shi tareda juyarda shi ita tadawo saitin dutsen, dutsen ya sauka akan bayanta wani kalan mugun kara tayi dan har kirjinta taji dutsen ta kankame Zayn sosai dashi kanshi saida yaji yanda dutsen ya daketa akirjinshi sanan ahankali tadago fuskanta ta kalleshi hada idanu sukayi shima kallonta yayi da idanunshi daya dayake iya amfani dashi,

ahankali tasakeshi sanan yafita daga kirjinshi sanan tawani juya takalli Lamido dake tahowa yana dariya yace “Au kin tsaya kin ci saa bullets dina sun kare da wlh nai wasting rayuwanki, Shegiya akwai, sai shegen wayau uwa yar dula” dan murmushi tayi da kyar sanan ta tsugunna kasa ahankali dutsen daya jefomata ta dauka sanan ta kalleshi yana dunfaro su yana tafiya yana dan dingishi saitashi tayi tadage da duka karfinta jefamai dutsen tayi dudda yaso ya kauce amman saida dutsen ya sauka akan goshinshi haba sai jini, wani kalan tsalle Farrah tayi tareda mai gwalo dayasa Zayn yadan ware idanunshi  cikeda mamaki, dan juyowa tayi takalli Zayn dake tsaye yana kallonta kaman yasami tv baki tabude kaman zatamai magana jin sahun gudu yasa duk suka kalli wajen, su Oga kezuwa but still sunada nisa hannun Zayn mara lafiyan takama suka shiga gudu daga ita har shi wanan karan yamafi na dazu, sunyi gudu nakusan 10min sanan suka kai wajen wani rami da bishiyoyi suka kare bazaka taba sani da rami a wajen ba, tsayawa gaban ramin tayi tana haki sosai sanan tasaki Zayn tanunamai ramin da hannu alamun ya shiga, ramin ya kalla sanan yakalleta dan bola nema cikin ramin, sake nunamai tayi tana kallon bayansu dan yanzun nan su Oga zasu cimmusu ganin inda take kallo shima baison akamasu yasa yashiga ya tsugunna yana taushe hanci amai na tasomai, juyawa tayi da sauri ganin ya shiga ciki zuwa gaban wani bishiyan mangwaro duk Zayn na kallonta wani kalan tsalle tayi tahau bishiyan sanan ta karyo babban reshe dakeda ganyayyaki da mangwaro nunannu ajikinsu,  da wasu different itace sanan ta dirko kasa ta taho da gudu fadawa cikin ramin tayi daidai su Oga sun karaso wajajen ahankali tasa reshen tarufe saman ramin dasuke ciki, ganyayyakin suka rufesu sanan ahankali tajuyo takalli fuskan Zayn dake kallonta, hannunta ahankali takai tadaura kan lips dinta alamun yay shiru, samin kanshi yayi da gyadamata kai ahankali kaman wani obedient child, sanan takalli hannunshi dataga yadaura hannunshi mai lafiya akai yarike kana gani kasan hannun azaba yakemai, ijiye itacen data karyo daga bishiyan tayi akan jikinta sanan takai hannayenta ta kwance igiyan hulanta tacire hulan shima ta ijiye akasa, ahankali tasaka hannunta tazame dan kwalin atamapan dake kanta wani kalan zubewa tulin churdadden gashinta yayi daba gyara abaya da Zayn yagani yana taba har kasan wajen dasuke zaune, ko kadan bata damuwa, yaga dan kwalin yaga tayi tararaba shi, sanan tadago kanta takalleshi hada idanu sukayi ahankali takalli monkey jacket din dake saman white shirt din dake jikinshi, da hannu ta nunamai monkey jacket din sanan tamai alamu yacire kallonta yayi dan baigane metake cewaba, hakan yasa ta daura hannunta kan jacket din tadan ja alamun yacire, dan yunkurowa yayi sanan yacire da kyar yabata, karba tayi sanan ta dukunkune rigan takai saman bakinshi duk yana binta da idanu, sanan takama hannunshi mai lafiya tadaura akan rigan asaman bakinshi sanan tanunamai saman ramin dakuma nunamai alamu yay shiru ma’ana kada yay ihu ya taushe bakinshi kada mutanen nan suzo sujisu, sanan ahankali yaga tasaka duka hannayenta kan hannunshi karyayye takama runtse idanunshi gam yayi koyaya aka taba hannun shi kadai yasan yanda yakeji,  ahankali take taba hannun ta lumshe idanunta, ta iya gyara karaya awajen maman ta takoya, Mamanta na gyara karaya sosai kusan shine ma aikin datakeyi a birni ana biyanta tana dauri agida, ita kawai gani tayi ta iya a kauyen nan tama mutane biyu dauri kuma sun warke, gano karayan tayi hakan yasa ta bude idanunta tadauki itacen data ijiye akasa ta daura kan jikinta sanan tawani kalan murde hannunshi tahade kashin dayasa yay wani ihu bakinshi taushe gumi na ketomai tako’ina, sanan ta jera itacen tass kafin tasaka igiyoyin dan kwalinta ta daure hannun layi layi tam tam, sanan tasaki hannun nashi ahankali bude idanunshi yayi yakalleta harta dauki hulanta tana daurawa akanta tana kulle

igiyan a gemunta, dayan igiyan daya rage ta dauka shi yanada fadi sanan ta kalleshi bayan tagama gyara zaman hulanta, tasowa tayi tazo da gabanshi takalleshi sanan tadaura hannunta daya kan idanumta, kafin ahankali takai igiyan tadaura ma idon mara lafiya tadaurea kullin abayan kanshi sanan  takoma tazauna, wani kalan dadi yaji da idon namai kaman zai fadi yanzu saiyaji kaman abu yatare idon daga fadi, ahankali yakalli hannunshi dudda yanamai zugi sosai but he's feeling much better kan dazu……… "bazasu taba wuce nan wajen ba kuduba dajin nan tass, duk inda za'agan su agansu, inba hakaba saina kashe kowa na kauyen su dan nasan daga rugar fulanin chan take, itane kaje kagani jiya da daddare Lamido" dasauri Lamido yace "a'a Oga, ni wata bazawara nasamu Oga".

This book is 500 VIP is 2k
3107021073 aisha Muhammad first bank pay and chat me up by clicking on this link;
wa.me/+2347012181461

💫 FARRAH💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣1️⃣
Cikin tsananin fushi dakuma tashin hankali Oga yace "Duk inda zaku shiga ku shiga kufito min da yaron nan, that boy life is our golden ticket to paradise" baisan ya akayi ba but jiyayi yasa hannu yakama hannun Farrah gam gam atsorace jin maganan da Oga keyi kirjinshi na bugawa dum dum dum! Ahankali Farrah takalli hannunta dataji ya kama yarike kafin gently tadago manyan idanunta takalli fuskanshi, ko kadan hankalinshi baya kanta fuskanshi na kallon sama dan asaman kansu yakejin maganansu gani yake kaman zasuyi missing step kawai su taka reshen mangwaron su fado cikin ramin dasuke su gansu su kasheshi, zufan dakebin gefen fuskanshi ta kalla dan murmushi tasaki tunda tai wayau yaune rana na farko data taba haduwa da namiji matsoraci, ko Baffa dayake nan siriri baikai Inna kiba ba baida tsoro, rashin mutuncin yake surfafama Inna dudda idanma duka ne zata iya zauneshi ma amman baya tsoron ta balle uban kowa, su Moddibo dabama sukai wannan girma ba suma basuda tsoro amman jibi wanan katon yanda jikinshi ke rawa, tabe baki tayi tadauke kai batare data cire hannunshi daga kan hannunta ba ta jingina da bangon ramin hankalinta kwance ta lumshe idanu dan wani kalan baccin gajiya takeji ko minti uku batayi ba bacci yay awon gaba da ita azaunen, minsharin dayaji taja yasa dasauri yajuyo da kanshi ya kalleta bacci take azaune bayanta jingine da bango tadan dukar da kanta hakan yasa bama ya iya ganin fuskanta sai saman hulanta, mamaki ne ya kasheshi how can she sleep comfortably acikin rami akan wanan dattin? Yana nan inda yake yanajin duka neme nemen shi dasukeyi aka wani kalan tsuge da ruwan sama dayasa yaji sun

kwasa dagudu, kalan azababben kishin dayakeji yasa yabude bakinshi ahankali yanajin wani iri but ji yake idan baisha ruwan nan ba zai iya mutuwa, ruwan dake tsiyaya daga ganyayyakin nashiga bakinshi yana hadiya ahaka, saukan ruwan dataji kan fuskanta yasa tabude idanunta ahankali kafin taja hulanta baya tadago kanta ta kalleshi ruwa na fesowa a fuskanta shima kallonta yake, saikuma chan yamaida bakinshi yarufe ganin kaman yanda takeshan ruwan yake kallo, dan yunkurowa kadan tayi taja reshen gefe ta lelleka ganin basanan yasa ta matsar dashi gefe tafito sanan ta tsugunna gaban ramin tamikamai hannu ahankali yakalli hannun nata sanan gently yasaka mata nashi aciki yafito ahankali da taimakonta, mangwaron su ta katse daga jikin reshen sanan tamikamai guda daya kallon mangon yayi sanan yakalli reshen da bolan da aka rufe dasu yanajin amai na zuwan mai tuna ruwan dayasha amman aman yaki zuwa sanan ya girgiza mata kai, maida mangwaron tayi tarike tafara shan nata dan rawa yafara na sanyi dan ruwa ake mai karfin gaske ita ko ajikinta, tafiya tafara da sauri shima yabita yana tafiya da sauri har zuwa gaban dutsenta hawa sukayi sanan suka shiga kogon, waje tanunamai hakan yasa ya zauna akasan ahankali fita gaban kogon tayi sai yanzun nema gabanta yafadi duka tumakan su Shanu daya kawai tagani awajen yana yawo, wani irin kalan mugun faduwa gabanta keyi, dawowa ciki tayi ta zauna sanan ta kalleshi kaman yanda yake kallonta batace mai komi ba.

Ahankali yana kallonta yace “do you have phone please”? Kallonshi ta tsaya tanayi kuri hakan yasa gently yace “kinada waya”? Girgizamai kai tayi alamun batada shi, shiru yadanyi saikuma yasake dago kai yakalleta still tana kallonshi murya chan kasa yace “wani gari ne nan?” Da demonstration tagayamai ganin yanda ya tsaya kuri yana kallonta bai gane abinda take cewa ba yasa tamai alamun tana zuwa tamike tsaye tafice daga kogon bayan riganta yabi da kallo duk jini yabata dutsen da aka buga mata, sauka tayi daga kan kujeran ta kwasa da gudun bala’in sa’i karkaransu ana ruwan nan, direct gidan su Shafa tayi tana shiga taga Shafa ita kadai a kitchen tana soya manja zatai girki, ganinta yasa Shafa tasaki baki tace “yanzu da girmanki kika shiga ruwa kika jike haka Kurma?” Karasawa gaban Shafan tayi tasa hannu ta dagata daga kan kujera sanan tafara gayamata komi a kurmance Shafa nabin labarin tundaga farko har zuwa yanzu, saida tagama tass sanan Shafa ta zaga ta bayanta riganta ta daga ganin taji ciwo sosai yasa tace “waike Farrah maisa bakijin…..” Farrah bata bari takarasa magana ba ta girgiza mata kai sanan tamata alamu itadai tabata wayan, jim Shafa tayi tana kallonta tanason Farrah sama da tunanin Farrah but bataso Farrah taje tasa kanta a matsala, wucewa tayi ta shiga dakin Baban su, wata tsohuwar waya taciro wayan ma akashe tabama Farrah karba Farrah tayi tana murmushi sanan takama hannun Shafa suka fice daga gidan, suna fita ta tuna yanda yakeji tadawo cikin gidan dasauri dakin shafa tashiga ta dauki bargon Shafa dake kan gadon tafito Shafa tabita da kallo sanan tai shiru, gudu sukahauyi nan da nan sukakai wajen, shiga ciki sukayi yana zaune inda Farrah ta barshi sanyin gaske yakeji ya kankame jikinshi warware bargon Farrah tayi ta lullubamai ya sauri yarike bargon sanan tamikamai wayan da Shafa tabashi karba yayi dasauri yana kallon wayan yana dannawa ganin akashe, kugu Shafa tarike tace “kaga Farrah Kurma ce, kuma marainiya ce batada Baba batada Mama, yarinyar nan dakake gani batada gata akauyen nan wahala take, Allah ne kadai gatanta koma wa zaka kira ka kira sabida kafita daga hannunta banson kasamin kawa a matsala” tunda take maganan yake kallonta harta gama, kallon Farrah yayi da itama kallonshi take yanzu daman

kurmace, juyowa yayi yakalli Shafa ahankali yace “inane nan?” “Kauyen kudiri” tafadi kai tsaye, murya chan kasa yace “awani gari”? Ahankali tace “garin adamawa” kunna wayan yayi cikin ikon Allah ta kunnu saura one bar, ga service ma kara daya itama rawa take, number Papa yasaka yay dialing yaji ana you have one minute remaining shima ana maganan tana breaking wayan yafara ringing dauka akayi yaji muryan Mami hakan yasa dasauri yace “Mami” muryanta na breaking sosai tace “Hello, Hello” dasauri shima yace “Mami, Mami, is Zayn” duk tsayawa kallonshi suke yanda yake maganan yana fama da wayan yakaita baki yakaita kunne, Shafa tace “ka karamata volume haka Baba keyi idan kawu yakirashi daga binni” da sauri yasa a speaker shima da kyar yagane sabida bai iya amfani da wayan ba “Zayn is that you, muryanka nakej………”. Muryan Mami shi yafito ras awayan daidai wayan ya katse kati yakare, gyadama wayan kai yayi ahankali saiga hawaye sharrrrr yazubo daga idanunshi, ware idanu daga Shafa har Farrah sukayi suna kallonshi, dama kattan maza na kuka,  ringing wayan yashigayi hakan yasa dasauri yadauka yasa a speaker wanan karan murya Baban shi yaji kaman ma kuka Alhaji yake dan baya iya magana da kyau yace “Zayn dina kana ina are you okay”? Girgiza kai yayi kaman yana gabansu cikin tsantsan shagwaba yace “I am so scared Papa, please come and get me, I am scared” cikin wani kalan lallashi da so naban mamaki Alhaji yace “stop crying where are you tell me zanzo na daukeka” ahankali yace “kauyen kuduri adamawa state” “adamawa state Innalillahi we are coming with choppers gamunan, kafin nakaraso I am calling the governor na Adamawa stay with this phone okay, wherever you are they’re going to provide you with security, I am coming for you Zayn dina, your father is coming okay” gydamai kai yayi ahankali wani kalan zazzabi na rufeshi jin muryan iyayen shi, suka katse wayan hannunshi yasa akan fuskanshi ya share fuskan nashi tass, sanan ahankali yadago kanshi yakallesu hawaye yagani sun taru a idanun Farrah sosai tana kallonshi, hannunta Shafa takama tace “wuce mutafi tunda za’azo daukanshi wayan idan zai tafi ya ijiye mana anan zamuzo gobe mu dauka” dan kallonshi Farrah tayi kaman yanda shima yake kallonta kafin ahankali tafara tafiya tanabin Shafa dake janta suka fice daga kogon.

This is not a free book chat me up directly by clicking on this link;

wa.me/+2347012181461

💫 FARRAH💫

✍🏻M SHAKUR

Imagine yourself kina kwance a comfort na bed dinki kina duba pictures and videos na hadaddun atampopi kina gamawa kawai ki zaba, place an order, make payment akawo miki har gida batare dakin fita kinje kasuwa ba.

Imagine yourself in the middle of stress da kata kata na biki but you don't have to worry akan atampopin anko dan akwai wacce zata miki supplying nasu har gida?

Imagine yourself kina tunanin that perfect and best gift dazaki bama kawarki be it birthday gift, wedding gift, suna gift or just casual gift, and M Shakur told you Atampa ne!

Just picture it lokacin da za'a kawo miki atampan acikin wata lafiyayyen fine jaka za'a saka miki atampan akawo miki ba abakin Leda ba kaman yanda aka sabayi a kasuwa?? Sweet right?
What if M Shakur tagaya muku yau all imaginations, dreams dinan naku can become through by introducing ATAMPA REALM to you guys💃
ATAMPA REALM is an online store dake saida atampopi variety of them, daki bari, masu kyau, masu ado, wayanda ake yayi, akan kudi kuma kalilan don't you want that??
Atampa Realm are life savers, biki, akwati, birthdays or anything they come through and represent!! Ina gayamuku atampopin su makes statement🌹

All you have to do is give them a call 📞 +2348097573597

Ga wayanda basason kira you can chat them up a WhatsApp by clicking on this link:;
wa.me/+2348097573597

You can also follow them on Instagram by clicking on this link;
https://www.instagram.com/p/CiQcu1IoZ7c/?igshid=YmMyMTA2M2Y=

You can join their WhatsApp group by clicking on this link;
https://chat.whatsapp.com/CUmRWXy4evqLtOoYp3XmNt

EPISODE1️⃣2️⃣
Saida suka fita ta tsaya chak hakan yasa Shafa dasuke tafiyan tare tajuya takalleta, cikin fushi tanuna mata kogon tace "wai kinsan shi daga wani waje ne Farrah? Shi namiji ne Farrah ba kamar Yar uwanki datake mace ba, zai iya kare kanshi idan zasumai wani abu, banda ma haka ba yanzun nan agaban mu yay waya za'azo a daukeshi ba eh"? cikin kurmanci Farrah tanuna mata to su tsaya afara zuwa daukanshi kafin sutafi, zuciyanta yaki bata sutafi su barshi tausayinshi takeji sosai, sosai ran Shafa yabaci shiru tadanyi tanabin wajen da kallo sanan takalli Farrah tace "kinsan iya yawan abubuwan dakika fito dasu kiwo? Jibi chan saniya dayace kadai anan, Farrah so kike kisa kanki a matsala ko, meya kamata kiyi yanzu inace ba tumakan nan yakamata kije ki nemo ki tattarosu ki kada gida ba, kinsan wayanan dabbobin sune tattalin

arzikin Inna na duniya da lahira ko, wlh ko kasheki tayi wanan karan bazan damu ba babu abinda yashafeni, karma kizo wajena kina kuka ni kinga tafiyata" tawuce zata tafi kaman ance Farrah takalli gabas su Oga ne dukansu hudun suka bullo dawani kalan bala'in sauri tasa hannunta ta fizgo hannun Shafa bama tajira mezata ceba tajata suka shiga kogon jikinta na tsuma, itama Shafan faduwa gabanta yahauyi sosai dan lokacin da Farrah ta fizgota ta hango mazan da bindigogi a hannunsu, kallonsu Zayn yayi ganin yanda suka shigo da gudu suna shaking hakan yasa yadafa bango da kyar ya mike tsaye ya kalli Farrah itama kallonshi tayi sanan ta gyadamai kai alamun eh sune, cikeda bala'in tsoro Shafa tace "sune Farrah?" Gyadamata kai Farrah tayi hakan yasa Shafa tace "kozo muyi sauri mu fice mu gudu karkaran mu muboye achan ni wlh banso na mutu yau" tai maganan tana hanyar kofa tafice dasaurin ta kallon Zayn Farrah tayi sanan tamai alamun yazo sutafi ahankali yabiyota abaya, ganin sun fito yasa su Oga suka hau gudu suma gudu sukahau yi Shafa agaba Farrah abayanta, Zayn abayan Farrah suna saukowa dagakan dutsen da gudun su, harbi sukahau yi amman cikin ikon Allah ko dayansu bai sama ba har suka karasa saukowa, ganin Zayn baya iya gudu sabida hannunshi yasa dasauri Farrah takama hannunshi ahankali ya kalleta daura hannun tayi a shoulder ta sanan tafara gudu shima Zayn na gudu Shafa na gabansu tana famfala gudu, su Oga na binsu abaya sun kusan cimmusu, juyawa Farrah tayi ta kalli bayanta, ganin Oga na saita bindiga saitin Zayn dake wani kalan haki yana gudu yasa dawani kalan sauri tasaki hannun Zayn tawani irin hankadeshi yafadi ta tare bullet din sai gefen kirjinta wani irin kara tayi ! bullet na nan ne kaman garwashi dake tattare dawuka mai kaifi, the pain is so sharp da saikaji kaman kabar duniya chak Shafa ta tsaya jin ihun Farrah daidai Farrah tawani irin faduwa akasa jini nawani kalan bulbulowa ta inda aka harbetan, juyowa Shafa tayi ganin Farrah azube akasa yasa tawani kalan Kurma ihu. "Kurmaaaaaaaa!" Sanan tawani taho kanta dagudu ta tsugunna shima Zayn dake kasa tashi yayi da sauri yana kallon Farrah da bala'in mamaki na she just saved him yama kasa tabuka komi sai rawan da hannunshi keyi kawai, murmushi Oga yayi yana tahowa cikin tafiya na kasaita yace "perfect haka ake harbi nakoya muku saiti nakoya muku amman abanza yau kun wasting bullets abanza a hofi" wani kalan rudewa Shafa tayi yanda taga jini na bulbulowa Farrah na tari yasa tasa hannu ta dumbuzo kasa ta maka akan ramin bullet din tana kuka takalli su Oga tace "Allah saiya kashe ku kuma azzalum……" bata karashe maganan ba sabida wasu kalan jiniyan motocin yan sanda dasukaji na tashi ata ko'ina sanan ga mutanen gari sun fara bullowa sabida karan harbin dasuka dingayi dazu ko'ina ya amsa, gakuma karan helicopters kusan uku dayasa su Oga suka kalkalli sama jikinsu nawani irin rawa, cikin ihu ganin mutane yasa Shafa tace "ku kamasu su yan sanda sukazo kamawa masu kidmashin ne" mazan gari suka yunkuro hakan yasa suka kwasa da gudu daidai lokacin motocin yan sanda na shigowa dajin, dan sunada device dake tracking bullet kaman magnet ne zai kaika wajen da akwai bullet, ga jirage nayawo asama, wani kalan ajiyan zuciya yasauke yana kallon yanda Shafa ke jijjiga Farrah dake tari har lokacin idanunta sunyi jajir suna fitarda hawaye, wasu manyan sojoji suka taho da microphone suna kiran sunan Zayn. "Zayn Ganuwa are you here"? Shiru Zayn yayi dan at this point iyayenshi kawai zai gani ya mike tsaye, helicopter su yasauka daga nesa sosai a filin, Mami dakuma Baban shi yaga sun sauko daga ciki, da Uncle, dawasu manyan Doctors ganin su yasa yamike tsaye ahankali yafara tafiya.

Daga nesa Alhaji yace “Innalillahi Zayn dina ne haka, Zayn” wani kalan fadawa jikinshi Zayn yayi ya kankameshi sai kuka ahankali, tsayawa Mami tayi a gefe tasa bakin gyalenta tana share hawaye ganin yaronta is fine, da kyar Alhaji yasakeshi sanan yay cupping fuskanshi yace “kowaye yamaka Wanan abun I will not rest sai justice yay taking place” gyadama Baban shi kai yayi sanan yasaki Dad yajuyo yakalli Mamin shi budemai hannu tayi hakan yasa yarungumeta ahankali ita tama kasa magana jin jikinshi zafi yasa tadagoshi kafinma tai magana Alhaji yakamashi yakalli Drs din yace “mu tafi sai su dubaka a jirgi” shida Baban shi suka wuce Doctors din suka bisu abaya, ajiyan zuciya Mami ta sauke sanan ahankali tadaga kafanta zata wuce kaman ance ta kalli wajensu Shafa dake jijjiga Farrah da idanunta ke kullewa idanunta suka sauka kan wasu yara biyu da dukansu ke sanye da kayan fulani daya na kwance akasa ga jini duk yabata riganta daya na rikeda ita tana kuka sosai dawani irin sauri Mami tace “Alhaji!” Tsayawa Dad yayi sanan yajuyo dasauri Mami tai wajensu Farrah ta tsugunna kansu takai yatsunta biyu ta taba gefen wuyan Farrah sanan tace “we have a gun short injury, bring first aid kit for me” Mami tai maganan cikin sauri tana ihu sanan takalli Shafa dake kuka sosai tace “kanwarki ce Ya akayi aka harbeta”? cikin kuka sosai Shafa tace “garin taimakon danku ne!” Chak Mami ta tsayar da abinda takeyi takalli Shafan, Gyadamata kai tayi cikin kuka sosai tace “tafito kiwo taga……..” nan takorama Mami labarin tassss wani iri jikin Mami yayi daidai one of the Doctors yakawo first aid kid, Ahankali tadago kanta takalli Zayn dake kallonsu yana tsaye tareda Baban shi sanan tasa hannu ta karbi first aid kit din tabude tawanke kasan da Shafa tazuba awajen tamata allura daidai Malam dashima yaji labari abinda ke faruwa awajen garinsu yataho wajen ganin Farrah ga likitoci akanta yasa da sauri yataho wajen yace “Maiya sami Farrah Shafa’atu”? Daidai lokacin Mami tagama abinda take tadago takalleshi sanan tamike tsaye ahankali tace “kaine mahaifinta Malam”? Girgizama Mami kai Malam yayi ganin babban mace yace “a’a diyar kanwata ce, marainiya ce babu uwa babu uba saini kadai” wani abu Mami taji ya tsayamata arai, anatse tace “an harbe diyarka garin kokarinta na taimakon d’ana, inaso idan ka yarda mu tafi da ita asibiti dole amata aiki acire bullet din, zaka iya biyomu idan yaso idan taji sauki sai adawo daku” kallonta Malam yayi sanan yabi yan sanda da sojoji da jiragen dake yawo asama, da wanda yake akasa, da yaron dayaga an lullube da bargo nai kyau yana tsaye kusada mahaifinshi dasuke kama wanda kana gani kasan shine yan kidmashin din suka kama daga ganinsu kaga yan birni masu kudi, ba yan yankan kai bane tunda ga yan sanda, lokacin yin kudinshi yayi yasan idan aka gama aikin zaa dawo dasu dole abasu kudi dayawa hakan yasa yace “to muje” wani gado aka kawo aka dauketa akai jirgin da ita suka shiga Mami na kusada ita tana monitoring heartbeat nata shikuma Zayn na zaune kusada Baban shi yay lakur ajikinshi sauran Drs na dubashi, shikuma Malam na zaune kusada yan sanda ya kankame jikinshi yanaji kaman Zai shide jinshi asama, tass Dr yaduba hannun Zayn sanan yakalli Alhaji yace “waya maka daurin hannun nan koma waye really saved his life daurin yayi kyau sama da wanda mu zama mumai a asibiti, idanunshi ne kawai needs work” ahankali Alhaji yace “waya maka daurin hannun?” Farrah yanuna murmushi Alhaji yayi yace “I will makesure I reward her awesomely for helping my son, for giving her life for you, me kakeso abata” murya chan kasa yace “anything” wani mugun kallo Mami tamai ita kanta tarasa gane kan wani kalan yaro ta haifa yanzu inda bataga Yarinyar nan ba da haka Zayn zai barta tamutu yarinyar data taimakeshi ta karbi bullet that was meant for him, ace Zayn yakasa fadi an harbeta adubata shi

takanshi yakEe, ajiyan zuciya tayi ta zubama fuskan Farrah idanu.

💫 FARRAH 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 1️⃣3️⃣
Direct wani babban asibitin da Mami ke aiki suka wuce dasukakai Abuja, jikin manya manyan likitoci har rawa yake aka wuce wani observation room da Zayn, dakin daza'ayi mai general check up kafin eye Doctors suganshi, Mami kuma scrubbing in tayi dan itace in charge surgeon ma Farrah she just feel this is the least she can do for the small brave girl after saving her son's life, shikuma Alhaji zama yayi acikin wani executive lounge da only VVIP guest dinsu ake bamawa, Malam dai yadawo dan kallo yana tareda su amman bai zauna akan kujeran da Alhaji da Uncle ke kai ba dan sunmai wani kalan mugun kwarjini yana kujeran dake bayansu, kaganshi zaka dauka wani almajiri ne, ringing da wayan Alhaji yayi yasa ya farka daga zurfin tunanin dayakeyi dasauri yadauki wayan ganin Gwamnar Adamawa ne ke kiranshi, amsa wayan yayi sanan yay murmushi yace "Alhamdulillah, thank you excellency, to to to shikenan" zare wayan yayi daga kunnenshi ya katse sanan ya kalli Uncle dake kallonshi yace "ankama daya daga cikin kidnappers din" dasauri Uncle yace "Alhamdulillahi naji dadi sosai Yaya" shiru Alhaji yayi yanadan karkada kafa yana tunani sanan yace "zan iya yafema mutum duk wani laifi dazai iyamin aduniyan nan dakake tunani amman banda laifi daya shine cutar mini da Zayn" yasakeyin shiru saikuma ya bude malummalum dinshi yadauko wani clean handkerchief yakai kan idanunshi yana share hawayen dasuke fitowa yace "inda sun kashemin Zayn da yaya zanyi da rayuwata eh" kama kafanshi Uncle yayi yace "Yaya dan Allah kadaina kuka nace kuma kadaina maganganu haka bagashi yanzu an ganshi ba" cikeda damuwa da rauni yace "inda yarinyar chan bata taimakeshi ba, da yanzu shine yake kwance a operation room rai a hannun Allah, you know something I am going to reward that girl handsomely wallahi kuwa" sanan yajuyo yakalli Malam dake dunkule waje daya sanyin AC ya isheshi yace "Malam kome kakeso kafadamini zan maka shi dan diyarku ta chanchanci sama da haka awajena mekake so kanason gida a birni"? Wani kalan washe baki malam yayi yana murmushi azuciyan shi yace "inama tamutu su biyani diyya nafi kowa kudi a kauyen mu" anatse yace "a'a Alhaji Baran iya rayuwan binni ba, kawai dai kudi nafiso na gyara gonata da sauran ayyuka" murmushi Alhaji yayi yace "tom shikenan zan saya maka gona dai dai gonaki dari a kauyen ku" wani kalan zaro idanu Malam yayi yakasa gasgasata maganan dayaji gonaki dari yajiance sanan Alhaji yace "zan kara maka da naira miliyan goma kaje kaja jari" wani kalan fadowa yayi daga kujera yay rarrafe yazo gaban su Alhaji, kwanciya yayi flat akasa yana kuka yana musu addu'a, murmushi Alhaji yayi yace "tashi kaje ka zauna" sanan yakalli Uncle yace "jeka kawo cash na 10M kabashi" dasauri Uncle yace "nadauka sai an sallami yarsu za'a bashi", girgixamai kai Alhaji yayi yace "kawomai miliyan gomanshi a leda kabashi yazauna yana kallo shima yanajin farin cikin da sanadin diyarshi nima inajin kalan farin cikin nan yanzu ahaka. "Kaico! Wayyoo Alhaji,

aradun Allah zuciyata zata buga, yau ni Malam nine mai da miliyan goma, Wayyoo Allah na" dan dariya Alhaji yayi sanan yatashi yawuce dakin da Zayn yake ciki shikuma Uncle yatashi fuuu yafice ko kallon Malam baiyiba Malam kuma sai sumbatun kudaden daya samu yake.

Yana zaune awajen Mami tafito tana sanye da kayan operation, tashi Malam yayi dasauri ganinta yace "ta mutu ne"? Turus Mami tayi tana kallonshi tambayan yamata bambaran akunne amman takakalo murmushi tace "bata mutu ba, kuma Alhamdulilah mun samu mucire kwayar bindigan nan da yan awanni zata farka zomuje kaganta" gyadama Mami kai yayi sanan tai gaba yana biye da ita abaya zuwa dakin da Farrah keciki, tana kwance kan gado da kayan operation ajikinta, kanta sanye da hulan operation, an rufamata bargo zuwa cikinta, daga wuyanta kana iya hango katon plasta da aka manna a kirjinta inda akai aikin, ga oxygen a hancinta tana fitar da numfashi tana saukewa, wani kalan bakin ciki Malam yaji daya ganta shi da yanzu zata mutu dayaji dadi daya huta daman ta zamemai nauyi aka, yanzu tamutu zai sami kudin diyyanta sanan yahuta da fitinan Inna, dan kallonshi Mami tayi itadai batasan ko kawai she's seeing it out of paranoia bane but the man doesn't look happy to see yarinyar tai surviving surgery, to anya ma uncle dinta ne as he claim kuwa,  anatse Mami tace "kace ba kaine mahaifinta ba"? Janye idanunshi yayi daga kan Farrah cikeda kauyanci yace "eh hasalima haryau ba'asan mahaifinta ba duka kauyen mu" ahankali Mami tace "Maman ta fa kace tarasu"? Gyadama Mami kai yayi yanadan tabe baki yace "mahaifiyarta dani kadai iyayen mu suka haifa, tunda tafara fita binni tana saida nono ta lalace, hartazo tagudu muka nemeta muka rasa, rana daya kawai tazomana da durmeme ciki kauye, wai ita tai aure amman mijin ya gudu yabarta todai a kauye ta haifesu yan biyu, yan kauyen mu suka tasata agaba tai cikin shege tazo tana karya cikin sunna ne da aurenta akanta, shine ta tattara ta gudu da yaran tasake barin kauyen, bata kara dawo da yaran ba saida sukai shekaru shadaya aduniya ta dawo dasu gida tana ciwo sosai da kauye yadauka ciwon kanjamau ta kwaso ayawon Duniya shine tadawo, babu kalan kunyan duniya da uwarta bata sakani ba, Toh dai ahaka ta mutu ciwon shine ajalinta, yaran suka dawo hannuna, bata wani dade da mutuwa ba yayan wanan ma ta mutu" yanuna Farrah, ahankali Mami tace "Allah ya jikan su da rahama" hakanan taji Farrah tabata tausayi taga tabon duka daban daban ajikinta yafi akirga wanda kana gani kasan clearly is the case of child abuse amman dai tai shiru, ahankali tace "bari nadan je chan wajen su Zayn naduba shi zaka iya zama da ita, dazaran ta farka bayan kwana biyu idan taji sauki za'a maidaku" "to Hajiya angode Allah saka da Alkhairi, Allah yakara girma" fita Mami tayi security dake gaban dakin tama whispering. "I don't trust him, keep an eye on him please" yes Ma ya amsa mata  sanan tawuce.

Kujera Malam yaja ya zauna yana kallon Farrah, kaman yadauki filon nan yadanne mata fuska tamutu yahuta yakeji, yana zaune ahaka ya saka ya warware shi kadai aka bude kofan dakin, Uncle ne rikeda Leda baka wani irin tashi Malam yayi yace "wayyo Allah kudade na sunzo" kafin ma Uncle yabashi kudin ya karba yana leka ledan saikuma ya rungume kudin yana hawaye wani kallon wulakanci da raini Uncle yamai sanan yawuce yafita daga dakin yawuce dakin

Zayn.

Kallon kudin Malam yayi sanan yakalli Farrah yace “tunda yanzu ga miliyan goma na a hannuna chass ni nama yafe gonaki darin na gudu abina ko, Allah yabani miliyan goma daga sama babu abinda nayi tasha kawai zani nakoma kauyen mu, Wanan kuma idan sunga dama su yardata kosu dawo da ita kauyen mu su suka sani koba hakaba” yana gama tunanin yawani mike tsaye ledan ya ijiye kan kujera yadauko bandir daya na kudi yakirga dubu goma yasa a aljihu sanan ya daure bakin ledan ya makaleta a hammata gam gam sanan yabude kofa yafice, fita yayi daga asibitin batare daya hadu dasu AlhaJji ba yana fita motan daya gani yatare yace akaishi tasha.

Imagine yourself kina kwance a comfort na bed dinki kina duba pictures and videos na hadaddun atampopi kina gamawa kawai ki zaba, place an order, make payment akawo miki har gida batare dakin fita kinje kasuwa ba.

Imagine yourself in the middle of stress da kata kata na biki but you don’t have to worry akan atampopin anko dan akwai wacce zata miki supplying nasu har gida?

Imagine yourself kina tunanin that perfect and best gift dazaki bama kawarki be it birthday gift, wedding gift, suna gift or just casual gift, and M Shakur told you Atampa ne!

Just picture it lokacin da za’a kawo miki atampan acikin wata lafiyayyen fine jaka za’a saka miki atampan akawo miki ba abakin Leda ba kaman yanda aka sabayi a kasuwa?? Sweet right?
What if M Shakur tagaya muku yau all imaginations, dreams dinan naku can become through by introducing ATAMPA REALM to you guys💃
ATAMPA REALM is an online store dake saida atampopi variety of them, daki bari, masu kyau, masu ado, wayanda ake yayi, akan kudi kuma kalilan don’t you want that??
Atampa Realm are life savers, biki, akwati, birthdays or anything they come through and represent!! Ina gayamuku atampopin su makes statement🌹

All you have to do is give them a call 📞  +2348097573597

Ga wayanda basason kira you can chat them up a WhatsApp by clicking on this link:;
wa.me/+2348097573597

You can also follow them on Instagram by clicking on this link;
https://www.instagram.com/p/CiQcu1IoZ7c/?igshid=YmMyMTA2M2Y=

You can join their WhatsApp group by clicking on this link;
https://chat.whatsapp.com/CUmRWXy4evqLtOoYp3XmNt

EPISODE 1️⃣4️⃣
Sai bayan sallan isha'i Mami da Alhaji suka taho dakin da Farrah keciki, ganin babu Malam adakin yasa Alhaji yace "why is she alone ina Uncle natan yake"? Yay tambayan yana juyawa baya, bodyguard dinshi dake biyedashi yasa kiran security itakuma Mami tai gaban gadon tana duba vitals din Farrah, shigowa security yayi Alhaji yace "ina Uncle dinta yake ko yaje masallaci ne"? Girgiza kai security yayi yace "I think he left" ko ita Mami dake shirin yima Farrah allura saida takalli security dasauri tace "left kuma"? Gyadamusu kai yayi yace "after kince I should keep an eye on him daya fita nabishi, anan gaban asibiti yatare mota yace akaishi tasha" dan murmushi Alhaji yayi yakalli Mami yace "are you sure dan uwanta ne kuwa"? Gyadamai kai Mami tayi tace "eh, I think she's a burden to them saisa daya sami kudi ya gudu, ko dazu I told the security to keep an eye on him cus I get this feeling kaman baiso tai surviving ba" girgiza kai Alhaji yayi yace "mutane kenan basusan yara rahama bane, Allah ya kyauta, how is she yanzu?" "She is fine, I will stay with her saika tafi gida da Zayn ko" gyadamata kai yayi yace "okay, I will tighten the security here no more taking chance dan kowaye keson hurting dina yanda Allah bai bashi galaba kan Zayn ba bazai taba hutawa ba sai burinshi yacika, be careful okay, if anything come up ki kirani" gyadamai kai tayi tana murmushi shima murmushi yamata sanan yawuce yafita zuwa dakin da Zayn yake, har yay wanka ya chanza kaya zuwa wasu simple top da short masu kyau farare dasuka bala'in amsanshi, yasaka wata dark blue wool hula dayama fuskanshi kyau ka kalleshi saika kara kallonshi, farin designers socks yasaka dawani vintage slippers mara hanci kana ganinshi kasan sanyi yakeji, babu abinda yasami idanunshi amman saida aka wanke idon akai plasta gobe zasu dawo abude idanun, murmushi Alhaji yayi ganinshi yanda yay kyau dudda har yanzu bai dawo daidai ba jikinshi ya bala'in nuna yaci duka sanan ya wahala, hannunshi Alhaji ya kama yace "let's go home, but first muje kama maman ka  sallama ko" cikin Wanan muryan nashi na baison yin magana yace "is she not going home da mu"? Girgizamai kai Alhaji yayi yace "nooo, Uncle na yarinyar yagudu cus I gave him 10M, kasan ur Mom is the most generous woman dana sani aduniyan nan, she offers zata zauna da yarinyar" shiru Zayn yayi bai kara cewa komiba, hannunshi Alhaji yaja yace "muje to" binshi yayi suka fara tafiya tare ahankali har sukakai dakin.

Budemusu kofa bodyguard yayi suka shiga cikin dakin daidai lokacin Farrah ta kwaye baki tafashe da kuka cikin bacci batare data bude idanunta ba, ahankali tadaga hannunta takai inda akai mata aikin aka rufe da plasta tafashe da kuka sosai cikin wani kalan siririyan murya da dakin yake echoing yana amsawa idanunta a lumshe har lokacin tana kokarin sosa wajen da aka mata aikin.

Dawani kalan sauri Mami dake zaune kan kujera ta tashi hannunta tasa da sauri tarike hannun Farrah datakai wajen tace “Allah sarki sorry, sannu kinji yafara mata zafi wajen, alluran yafara sakinta sannu karki taba” kara karfin kukanta tayi dayasa for the first time Zayn Zayn da suna shigowa dakin yanemi waje kan coach na dakin ya zauna yana danna sabuwar wayan da Baban shi ya kawomai dan dayan tabace yadago kanshi, gently kaman wanda bayaso yadaura idonshi akanta, blue operation net cap din da aka samata yadan zame baya haka ya bayyanar da dark curkudadden black hair dinta, gashin goshinta sun kwanta tass tass sunyi wani kyau, kodan sabida kalan hasken wutan dakin ne oho but wani kalan haske tayi sosai kaman baturiya idanunshi a rufe ruf amman lafiyayyun hawaye ne ke fitowa daga cikinsu bana wasa ba, wasu nabin gefe suna hanyan kunnenta wasu na gangarowa kasa, dogon hancinta har kyalli yake sabida maiko, ta tabe baki sosai irin yanda bakin mai kuka keyi, lips dinta sun tattare sun bushe sunyi pink yirrrr, baisan mesa ba tunda yake arayuwanshi baitaba jin urge na kaman yacema mutum sorry ya lallasheshi ba sai yau, kaman tausayi tabashi ne ko she looks innocent ne oho, ganin understand what exactly yakeji is hard for him yasa yadauke kanshi da sauri kaman ance yadaina kallonta yamaida hankalinshi kan sabon wayanshi yana daddannawa.

Dayan hannunta tadaga zatakai kan ciwon jin anrike hannunta tana kuka sosai Mami tasake rikewa hakan yasa da sauri Alhaji yazo gaban gadon yace “mesa takeson ta taba wajen aikin”? Murmushi Mami tayi tamikamai hannunta daya tace “tayani rike hannun nan kaga” karban hannun Alhaji yayi yarike yana kallon Mami, Mami takai hannunta kan fuskanta tashare hawayen dake gangarowa sanan ahankali kaman mai whispering tace “dazafi”? Gyadamata kai Farrah tayi ahankali still idanunta a rufe, satan kallonsu Zayn yayi saikuma yasake dauke kai, ahankali Mami tace “kin tashi”? Gyadamata kai tasakeyi kaman Yar yarinya alamun eh, murmushi Mami tayi tace “meke miki ciwo yanzu to”? Shiru tayi batace komiba cikin lallashi kaman tana magana da Yar yarinya Mami tace “fadamin sunan ki inji” shiru tayi batace komiba still. “She can’t speak” Zayn yafadi ahankali batare daya kallesu ba yana danne danne awayanshi, daga Mami har Alhaji dasauri suka yakalleshi, Alhaji yace “kaman ya she can’t speak”? Dan yatsine fuska Zayn yayi batare daya kallesu ba har lokacin yace “she is dumb Daaaad” yay maganan irin yafara gajiya da tambayan su dinnan, “kurma”? Alhaji yafadi dasauri, gyadamai kai Zayn yayi yadan kallesu yace “the girl that was with her told me she can’t speak at all” maida hannunta Mami tayi da sauri ta ijiye akan gado, sanan tajuya da sauri tafita daga dakin batare datace musu komiba, bata wani jimaba tadawo dawani torchlight karami a hannunta, fuskan Farrah ta taba ahankali tace “Farrah” dan motsi Farrah tayi, murya chan kasa Mami na shafa gefen fuskanta tace “budemin bakin ki nagani” tai maganan tana bubbuga gefen fuskanta dan har yanzu bata gama farfadowa daga alluran ba, ahankali tabude bakinta, haska bakin Mami tayi saida takoma baya hakan yasa da sauri Alhaji dake tsaye kusada ita yace “menene”? Ajiyan zuciya tasauke sanan tama Alhaji alamu da idanu yazo yagani sanan yakoma baya yace “why is her throat that black”? Maida mata bakin Mami tayi tarufe sanan cikin harshen turenci tace “this girl has been suffering, this is clearly a child abuse case, Alhaji kaga tabobin duka ajikinta kuwa? Kaga bakin nan nata garwashi aka samata awuya is not like she can’t speak, ita kanta batasan she can speak ba sabida tsoron azaban datasha lokacin da aka

samata garwashin" yanda idanun Alhaji sukaija zakasan ranshi yabaci ainun, cikin fushi sosai yace "me wanan Yar karaman yarinyar tamusu daza amata irin wanan zalincin garwashin wuta a wuyan mutun? Eh? Sunsan menene y'ay'a kuwa sunsan cewa rahama ne su, why will people be so wicked and cruel, wlh wlh saina kullesu, zasu fadamin meta musu aka mata haka, let's go Zayn" sanan yajuyo yace "make sure taji sauki kinji wife" gyadamai kai tayi sanan suka fice yarufo kofan itakuma Mami ta zauna ahankali kan kujera tai folding hannunta akirji tana kallon Farrah, batasan kodan sabida ta taimaki Zayn bane but hakanan taji she's growing strong affection for yarinyan, ga yarinyan is so fine, very fine beautiful girl, gata Yar karama duka duka yarinyar nan bazata wuce 17/18 ba,how can you be wicked to this small girl.

Wani kalan kuka Farrah tafashe dashi sosai cikin baccin dayasa Mami takara tashi, hannayenta takama ahankali tana kiran sunanta. "Farrah, Farrah, gani nan" wani kalan yunkurowa Farrah tayi cikin bacci tawani kalan rungume Mami kamkam cikin wata kalan little voice tace "uhnnn Maa….m" wani kalan lumshe idanu Mami tayi ahankali takai hannunwanta tadaura abayanta tana bubbugawa jin takirata da Mama almost 1min sukai ahaka sanan Mami tamaidata ta kwantar da ita, murmushi tayi taja bargo tarufa mata da kyau sanan tawuce bayin dakin alwala ta daurOo tazo tasa hijabi ta shimfida dadduma tai nafila sanan ta kwanta akan lafiyayyen massaging chair dake dakin ta Minat da kafafunta.

EPISODE 1️⃣5️⃣
Wuraren 6 nasafiya tashiga bude idanunta dasuka mata nauyi sosai sunyi tsami, da kyar take budesu kafin takarasa budesu gabaki daya tanabin saman dakin datake da kallo dakeda haske mai kyau, kodai tamutu ne ta tambayi kanta tana sake kulle idanunta sanan tabudesu ahankali kaman wacce ke kokarin tantance abu, ganin still dakin take yasa ta juyarda kanta tabi ruwan da ake kara mata da kallo zuwa hannunta da ake karama ruwan, yunkurawa tayi zata tashi zaune amman takasa sabida zafin dataji agefen kirjinta batasan lokacin data saki wani malalacin kara ba. "Asshhh" dagokai Mami dake kan dadduma tana lazimi tayi ganin Farrah ta farka yasa tai murmushi, shafe addu'an datakeyi tayi sanan ta mike tsaye ta taho gaban gadon, tunda tafara tafiya tana tahowa Farrah dake kwance akan gadon ta tsare Mami da idanunta dan ganin wata faran kyakkyawan mata tayi tanada dan jiki ba yarinya bace, tanada kyau na gaske kaman wata Yar arab, gawani lafiyayyen murmushi kwance kan fuskan matan tana kallon Farrah itama hakan yasa Farrah tace "to kodai tana aljanna ne" tsayawa Mami tayi gaban gadon daidai saitin kan Farrah sanan takai yatsunta biyu tadaura kan saman goshinta tana duba temperature dinta ahankali tace "kin tashi"? gyadamata kai Farrah tayi ahankali tana kallonta still kana ganin kallon kasan kallon na wanda bata sani bane kallon sabuwan fuska, ganin yanda Farrah ke kallonta yasa Mami tai murmushi tace "zaki zauna"? Gyadamata kai Farrah tayi dasauri hakan yasa Mami ta taba wani abu  gadon yadago Farrah ta zauna tana dan yatsine fuska sabida tsami da jikinta yayi, "jikin ki na ciwo"? Mami ta tambayeta ahankali, dagokai tayi ta kalli Mami batasan mesa ba samin kanta tayi da gyadamata kai ashagwabe kaman zatai kuka, murmushi Mami tayi takai hannunta guda biyu tai cupping face nata murya

chan kasa tace “duk zai daina nan bada jimawa ba, yanzu zakiyi wanka saiki salla, saikici abinci saina baki magani, kinajin fitsari”? Dasauri Farrah ta gyadamata kai, murmushi Mami tasakeyi tabata hannunta tace “sauko to muje” da taimakon Mami ta sauka daga gadon ahankali, slippers Mami tabata tasaka sanan suka shiga bayi, dakanta Mami ta hada mata ruwan zafi na wanka, sanan tasamata toothpaste a sabon brush dake bayin tace “ki brush saiki wanka, ina zuwa” Mami tafito daga bayin, fita tayi daga dakin tasauka kasa wani boutique dasuke dashi a asibitin tashiga, tundaga kan pant, wani pink gown, da black hula, da after dress Mami tasaya mata da cream, tabiya kudin ta taho, bra ne kawai batasaya ba shima dan bazata iya sawa yanzu bane sabida aikin da akamata, komawa dakin tayi, landline na dakin ta dauka tamusu order lafiyayyen breakfast asibitin babban gaske ne kaman hotel yanda zakai order abinci a restaurant na hotel haka asibitin ma yake, ijiye komi tayi sanan tawuce gaban bathroom din knocking tayi tace “kin gama”? Jin shiru yasa tashiga bayin tana zaune tagama wankan amman takasa daukan towel, kare kirjinta tayi a kunyace, towel Mami ta dauka sanan tazo inda take lullubeta da towel din tayi sanan ta dagata tashi tayi ahankali tarike Mami batada karfi ko kadan, fito da ita Mami tayi da taimakonta ta shiryata tsaf sai kunya takeji, pink gown din Mami tasamata daya amsheta da black hula, Mami tace “kinyi kyau” sata tayi tai salla azaune kafin ta idar an kawo musu abinci, gado ta dawo zama tayi Mami tabata tea ahankali ta karbi cup din tana kallon Mami, murmushi Mami tayi tace “baki sanni ba ko” Gyadamata kai Farrah tayi, murmushi Mami tasakeyi tace “sunana Mami” anatse tace “nine mahaifiyar Zayn, yaron dakika taimakamawa har aka harbeki tasanadin hakan, munzo dake asibiti nan Abuja tareda mahaifinki Baffan ki amman shi yatafi, yanzu kina wajena har kiji sauki karkiji tsoro kinji zan kula dake ni Maman kine kinji” Gyadamata kai tayi ahankali, murmushi Mami tayi tace “sha tea dinki to” tea takai bakinta saida ta tada kofin sanan tacire daga bakinta tabama Mami kofin, wani irin tausayinta Mami taji tace “nakara miki tea”? Gyadama Mami kai tayi dasauri, tea dinta Mami tamika mata karba tayi shima ta kwankwade, ahankali Mami tace “nasa akawo miki wani”? Girgiza ma Mami kai tayi alamun ta koshi, ajiye cup din Mami tayi sanan takalleta tace “fadamin sunan ki” kai tazo zata girgiza Mami tace “a’a bude bakin ki kifadamin da baki, naduba bakin ki jiya nasamiki magani, muryanki yadawo zaki iya kina magana yanzu, fadamin sunanki naji” ahankali tabude bakinta tana kallon Mami kaman yanda Mami ke kallonta, da duka karfinta da tsantsan kwazo da struggling da kai kanka dake kallonta zaka iya gani a kwayan idanunta ta danne idanunta tace “F…….Ffffff…………Farrrr……” bude idanunta tayi da sauri hardan zufa ya keto mata a goshi tsabagen kokari, murmushi Mami tayi sosai tace “sannu kinji, all you need is just a little therapy, amman kina magana, ke ba kurma bace, u can speak, karasa fadamin sunan naki inji” ahankali tace “Farrrrrr………..r……….rahhh” wani kalan huge smile Mami tayi tace “wowwww” itama Farrah murmushi tayi takai hannunta kan bakinta tana shafawa dudda sunan ararrabe takira but she was able tafadi sunanta yau, Shafa kadai take iya kira, itama da kyar take fadi, but yanzun nan tafadi ma Matar nan sunanta. “Kinji dadi?” Mami tamata tambayan ganin yanda take murmushi takira sunanta, kai ta daga zata gyadama Mami dasauri Mami tace “no, dabaki zaki amsani” dan runtse idanu tayi kaman yanda mai in’i’na keyi tace “e….h” murmushi sosai Mami tayi tace “good girl” wani strawberry smoothie dake cikin wani fine bottle da straw dinshi tadauka tasamata straw din tabata, ahankali tasa hannu ta karba cikeda dason gwada magana kuma tace “n……….a……g…..de” dan murmushi Mami tayi tana saka labcoat nata tace “kigodema Allah” tab dinta ta dauka ganin zata barta ita kadai yasa ta shiga

YouTube wani cartoon movie tasa mata sanan tabata, ahankali Farrah tasa hannun ta daya ta amsa dan sayan tana rikeda smoothie Mami tace “kiyi kallo bari naje naduba wasu patient ko, yanzun nan zan dawo kinji” zata gyadama Mami kai Mami ta girgiza mata kai alamun no hakan yasa tace “tttttt….o” murmushi Mami tayi tajuya tafita daga dakin, saida tamaida kofan tarufe sanan tasaukar da kanta ahankali bayan Shafa wanan ce mata tabiyu dake sonta aduniya, Matan kaman Maman ta, hawaye ne suka zubo mata daga ido dasauri tasa hannunta ta share sanan takai goran smoothie baki tafara zuka dadin dataji yasa tahau sha sosai tana kallon cartoon dinta ita kaman ma abarta a asibitin taitai zama.

Bude musu bayan motan bodyguards sukayi, ahankali yasauko daga motan yana sanye da Greg Lauren horizon print crew neck t-shirt, black color ne t-shirt din dakeda zanen rana ajiki da color na sunset, yasaka wani jean na Ksubi, frescobol Carioca round toe espadrilles (takalmi) yasaka, yauma wani Rick Owens sarka yasaka daya fito dashi yasauka agaban riganshi yana kyalli kana gani kaga dimond, fuskanshi har wani sheki yakeyi idanunshi sanye da bakin glasses na police sabida plastan dayake idanunshi, duk wanda ya kalleshi saiya sake juyowa ka kalleshi zaka dauka wani  musician ne yazo, agogon dake hannunshi ya kalla na Horus, ganin 11:15AM yasa yadanja gajeren tsaki, bayanda zaiyi ne yazo hospital dinan all he needs right now is to smoke and yasami mace, rabonshi dayasha taba tun ranan nan, fitowa Dad shima yayi daga motan waya a kunnenshi yana magana awaya sanan yasa hannunshi yaciro wani katon teddy  babba na lion king mai remote, idan kadanna remote din zaka dauka live lion ne yana tafiya sanan yay haushi, karasowa gaban Zayn yayi sanan yace “hold on Barrister lemme talk to my Son” cire wayan daga kunenshi yayi yakalli Zayn din, teddy yasamai a hannu yace “ga teddy daka sayama patient dinmu, jeka sami Mami ka Dr ka will see u daga nan I need to rush, one of the kidnappers da aka kama yay magana I need to go” yakalli bodyguard dinshi yana daya magana yace “go with Zayn” sanan yashafa fuskan Zayn din yace “bye son” ahankali yace “bye” sanan yawuce yana tafiya ahankali har zuwa gaban dakin da Farrah keciki, bodyguard din dake biyedashi yakalla yace “get me a pack of cigarettes” batare daya jira amsan shiba yabude kofan dakin yashiga ciki, jin anbude kofa an shigo dakin yasa Farrah tadago kanta da wuri hada idanu sukayi da Zayn daya kallo gadon dudda idanunshi nacikin bakin glasses but tsaf kallo daya Farrah tamai ta ganeshi, kafeshi tayi da idanu bata ko kyaftawa tana kallonshi kaman yanzu tafara ganinshi ganin ya chanza mata kaman ba mutumin jiya ba dahar kuka yake, yawani kara zama mata babba sosai a idanu kuma yay wani kalan kyau kara kallonshi take sabida sarkan dataga yasaka kaman mace, wani zirrrrrr yaji ajikinshi sabida yanda take Farrah ke kallonshi da manyan idanuwabta dake nan kar kar kaman madara dawani kalan sauri yadauke kanshi yakarasa shiga cikin dakin sanan yawani kalan defa mata teddy lion din akan gado tawajen kafafunta dasauri takalli teddy sanan ya jefa mata remote dinma da mistakenly ya danna remote din ya kunna teddy, Farrah dake kallon teddy ita Allah yasan bama tasan akwai abu kaman haka aduniyan nan ba, gani tayi teddy dake kwance kafanta yawani tashi tsaye lion din yana kallonta in the eyes, bala’in faduwa gabanta yayi, ganin yafara nishi yana bude bakinshi yay wani kuka tareda tsalle gabaki daya yasa daga pad da drink din datake sha duka tawani watsar dasu kan gado ta kurma ihu da Zayn dake zaune kan kujera yaciro wayanshi

yana dannawa baimasan abinda ke faruwa ba  yadago kanshi dasauri. “Aahhhhhh” wani kalan tsalle tayi ta dirko daga gadon tama manta tanada ciwo shima lion din tsalle yayo zai fado kanta wani wawan ihu tayi tama rasa inda zata fadawa kan dogon coach din da Zayn kezaune tayi tawani kalan fada jikinshi daga ita harshi fadawa sukayi flat kan kujeran yana kwance tana kwance saman jikinshi ta kankameshi gam gam jikinta nawani kalan rawa ta kulle idanunta, sake tsalle lion din yayi tareda haushi zaiyo kansu hannunshi da baida Ipy Zayn yasa chak yakama lion din yana kallon fuskanta yanda lips dinta ke bari, gabaki dayan hanuwanta ta rirrikeshi dasu, kafe fuskanta yayi da idanu yana kallonta is she scared? Ya tambayi zuciyanshi, tureta yashigayi daga jikinshi kin sauka tayi taki bude idanunta ta makalemai wuya alamun barata sauka ba, baki yadan bude cikeda kulewa yace “sauka daga jikina” kaman wacce ke tsoroOOn bude idanunta tabudesu tadaura idanunta kan fuskanshi hakanan jJi tayi gabanta yafadi dum!….

EPISODE 16

Dudda yana sanye da black glasses bata ganin kwayar idanunshi amman wani kalan cika mata idanu yayi gashi yana wani kalan kamshi da takeji kaman kada tasakeshi tunda take aduniyan nan bata tabajin irin kamshin dayakeyi ba Subhanallahi kamshin dadi, ganin yanda yabata rai yana jiranta ta sauka daga jikinshi yasa ahankali tashiga dagashi tana satan kallon lion din dataga yarike a hannunshi, komawa gefen kujeran tayi ta nannade kanta cikeda tsoro tana kallon hannun nashi dake rikeda lion din sai yanzu ma taji inda aka mata dinki namata ciwo, tashi Zayn yayi ranshi bace, kayan jikinshi ya kalla ganin yanda suka yamutse dudda bawani yamutsewan kirki bane amman jiyayi ranshi yabaci kallon Farrah yayi da itama daidai lokacin tasaci kallonshi wani dan iskan tsaki yaji. “Mtswwww stupid girl” yafadi ahankali ware idanu Farrah tayi jin yazageta bata wani jin turenci but tasan stupid tun a kauyen su wucewa yayi fuuu yafita daga dakin da teddy a hannunshi daidai bodyguard din daya aika siyomai taba nadawowa teddy yamikamai cikeda masifa yace “donate this teddy to children ward, apparently the stupid girl na tsoronshi” yay maganan yana fizge kwalin tabanshi yawuce waje jikinshi har tsuma yake yakosa yasha taban.

Shigowa dakin Mami tayi ganin Farrah zaune kan kujera yasa tace “Iyye kin sauko”? Kai Farrah tadaga zata gyadama Mami, Mami tai mata kallon no, hakan yasa tadan runtse idanunta tace “e……h” murmushi Mami tayi sanan yawo wajenta gefen kujeran ta zauna hannunta takama tace “nasan yanda kikeji, but idan zaki magana, relax, take it easy, kiyi maganan a sannu akuma hankali batare dakinyi tunanin komi ba, once kika koyama kanki kina amsawa da maganan nan da 2days zaki fara magana lafiya lau kinji” wanan karan bata lumtse idanu ba ahankali tace “ehhh” murmushi Mami tamata tace “ina Zayn, Dr shi na jiranshi” ahankali tana kallon Mami tace “f…….iiii…ta” “okay yafita waje, bari naje nakirashi muje ganin Dr, I am coming idan nadawo zamuje gida, zakije gidana”? Mami tamata tambayan cikeda so, wani cute smile tama Mami ahankali tace “eh” wucewa Mami tayi tafita daga dakin tana murmushi she so much love Farrah bama tasan mesaba.

Tana kaiwa gaban entrance din Zayn na zuwa wajen shima daidai yana yarda karan taban hannunshi wani kalan mugun kallo Mami tamai sanan kawai tajuya cus da mutane awajen binta abaya yayi zuwa office din babban likitan idanun wanda yake bature ganin Zayn yasa yau murmushi yace “Mrs Zayn I really like this your boy he’s so cute” murmushi Mami tayi tana kallon Zayn dako gaidashi baiyiba yawuce yay zamanshi kan gadon duba patient, tashi Dr yayi yazo yacire plasta idanun yana kallon idon yace “can you see me”? Kallonshi Zayn yayi yana ganinshi da idon amman ba sosai ba, murya chan kasa yace “I can’t see clearly with it” murmushi Dr yayi yadagashi yace “I expect that to happen, I made a glass for you dagakai amfani dashi for 3month, zaisa idanun su warke” yay maganan yana kawomai fararen glasses din, yasamai sanan yace “can you see me now” gyadamai kai Zayn yayi yana kallonshi Dr yay murmushi dan glass din yanamai kyau sosai kaman wani professional Dr dinan, Dr yace “that’s all” kaman jira Zayn yake yasauka daga gadon yafice, Mami ne ta kakalo murmushi tace “thanks Dr OP” murmushi yamata yace “you are welcome” fitowa Mami tayi Zayn haryadanyi nisa tace “Zayn” juyowa yayi jin Mami takirashi, anatse tace “to my office” tajuya tawuce, dan yatsine fuska yayi sanan yabiyota abaya, shiga cikin wani hadadden office tayi ta tsaya gaban kofan tana jiranshi shigowa yayi hakan yasa tamaida office din tarufe tasa key sanan tawuceshi taje ta zauna, agaban table dinta wasu kananun photo frames guda uku ne gaban table dinta daya na Zayn ne yana jariri, daya dayay graduating daga university dayan kuma hoto ta ne da Alhaji da Zayn tareda su, kujeran dake gaban desk din nabaki ya zauna ahankali tareda dan sosakai irin na yan iskan nan dan yasan fada Mami zatamai, Mami takai kusan 1min tana kallonshi yanda yakeyi tasan cewa yasan fada zatamai, tasowa tayi ahankali ta zagayo inda yake, dayan kujeran dake gaban desk din dake facing na Zayn din taja ta zauna ahankali tana kallon fuskanshi, cikin wata kalan tattausan murya tace “Zayn” dan dago idanunshi yayi yakalli Mami ahankali yace “Yes Mami” hannu Mami tadaura kan bakinta kaman tana kokarin taushe kuka ne komenene ma takeji oho kafin ahankali ta zare hannun tace “Zayn is this how you show Allah you are grateful daya ceceka yay saving rayuwan ke eh? Two days ago Zayn you were kidnapped, this is Abuja aka tafi dakai chan wani kauye wai kuduri a Adamawa inda badadan Allah yasa that girl” tanuna kofan office dinta, tace “that girl, dake kwance akan gadon chan ta taimaka maka tasamo maka waya munyi magana dakai ba hankalinmu ko tunanin mu bazai taba kawomana kanachan wata duniya Adamawa ba” Mami tai shiru sanan ahankali tace “Zayn you almost die, you almost lost your life, look at your hand” tanunamai hannunshi dake nan akarye an daure, tace “look at your eyes” tanunamai idanunshi dake sanye da glass, tace “look at your whole body an zaneka blue black, Zayn u remembered you were crying danai waya dakai kana fadamana you were scared Zayn harka manta” Mami tai maganan ahankali tana kallonshi, dan lumshe idanunshi yayi kana ganin yanayin shi kasan maganan ta shige shi, ahankali Mami tace “Zayn tunda kataso bakasan menene wahala ba but rana tsaka within just 48hrs Allah ya nuna maka akwai rayuwan da ita sunanta wahala, ukuba da tsantsan azaba, sanan yanuna maka dukiyarka is nothing bata isa ta ceceka ba alokacin dazai kamaka, sanan yanuna maka shi kaskantaccen mutum dabaka dauka a komi ba zai iya maka abinda babu wanda zai iya maka shi aduniyan nan, Zayn badadan this incident ba someone like that girl Farrah can not even come close to you cewa zakayi she looks scary sabida Yar kauye ce bata

da kudi irin na gidan Baban ka, Zayn did you know cewa second chance Allah yabaka" Mami tai maganan tana dafa knees dinshi, ahankali tace "Allah has given you second chance amman harka fara misusing nashi, kafara shaye shayen ka, mutum bai isheka da kallo ba, ba salla ba salati, babu wanda yakai matsayin kacemai kagode or thank you, did you thank that little girl that saved your life and took a bullet for you"? Mani tai maganan tana daga murya, shiru Zayn yayi kanshi akasa hakan yasa Mami ta dakamai tsawa. "Zayn did you thank her"? Ahankali ya girgizama Mami kai alamun no, wani kalan murmushi tayi tace "Baban ka nada kudi kafi karfi kama mutum godiya ko Zayn, you feel idan taji sauki u can give her money, jirgi and just send her off that's your thank you" Mami tai shiru tana kallonshi, takai kusan 2good minute kallonshi take idanunta sunyi ja kaman kai shirin kuka, ahankali tace "all this behavior naka Zayn is my fault, lokacin dazaka fara JSS1 da zaakaika outside I had the chance nace baza akaimin yaro wajeba anan gida agabana zai karatu but nai shiru nabiyema Allah kiri kiri inaji ina gani kaki dawowa Nigeria tundaga nan kana makale da baturiyan Nany dinka dake kula dakai achan look at you now Zayn at 26yrs old you can't differentiate between right and wrong, ba salla ba salati, ba komi, rayuwa kawai kake mara amfani magana ma sai anyi da gaske kakeyi, Zayn why why Zayn hmmm? Kataba tunanin inda munrasaka in this incident yaya zamuyi da rayukanmu dagani har Baban ka, why don't you wanna be a better person for the sake of son damuke maka eh" Mami tai maganan hawaye na gangarowa daga idanunta sharrrr, wani iri Zayn yaji dasauri ya kauda kanshi gefe tunda yake baitaba ganin Mami na kuka ba sai yau, sanyi jikinshi yayi ahankali yace "s……sorry Mami" girgiza kai kai tayi tace "I don't want you to tell me sorry, I want you to start doing the right thing, amend your ways ka koma ga Allah, kafara rayuwa kaman wanda yakeda hankali yay girma, someone of your age, kasakama wayanda suka maka hallaci da alkhairi Zayn, I believe in you, you are a very good boy Zayn I know that cus ni ne mahaifiyar ka kaji" kasa daurewa yayi yanda yaji Mami na kuka ahankali yatashi daga kan kujeran juyawa yayi ahankali yace "Mami I am sorry" hannunta tasa dasauri kan idanunta tashare fuska nata dan murmushi tayi tace "zonan Zayn" juyowa yayi ahankali yakalleta ganin ta share fuskanta yasa ahankali yaje gabanta, murya chan kasa tace "promise me you will change" ahankali yace "I promise Mami" murmushi tamai sanan tai pecking goshinshi tace "tashi kaje I am coming" tashi yayi yawuce yafita daga office din tabishi da kallo.

Ahankali yake bude kofan dakin da Farrah take, zaune yaganta yanda yabarta dazu akan dogon kujeran nan tana bacci ga wayanshi daya gani tarike a hannunshi, dawani kalan sauri yataba aljihun shi jin babu wayanshi yasa yadan yatsine fuska probably dazu ne ya manta dashi adakin, maida kofan dakin yayi yarufe sanan yazo gabanta ya tsaya hannunJhi ya mika mata yace "ke give me my phoOne".

EPISODE1️⃣7️⃣

Ganin ko motsi batayiba yasa yay dan gajeren tsaki yaduko yana kallon fuskanta, hannunshi yakai ahankali yadaura kan wayan yaja cikin bacci itama taja tarike wayan gam tanadan gyara yanayin zaman datayi cikin baccin taredayin hamma, fuskanta ya tsaya chak yana kallon yanda take hamman tareda yin dan nishi ahankali, she looks super cute baisan mesaba hakanan kawai yatashi batare daya karbi wayan ba yawuce yafita daga dakin zuwa motan shi

bodyguards biyu biyedashi, shiga motan nashi yayi da Dad yasa aka kawomishi danshi yafita danashi dasukazo dashi, zamanshi yayi cikin motan  tareda lumshe idanu, anytime yayi yunkurin lumshe idanu mutanen nan yake gani, ko jiya is because Dad ya kwana dashi ya iya yay bacci, the whole experience yadameshi yahanashi sakat, dan tsaki yaja yasa hannu a aljihun shi yadauko kwalin taba daya yazaro sanan ya kunna da sauri yashiga sha tareda kwantar da kanshi jikin kujera, he's feeling so dull the only thing dayake bukata yanzu is to be extremely high and have a wild sex.
Kiran sallan zuhur akayi a masallacin dake nan cikin hospital din, dan yatsine fuska yayi kaman yay ignoring karyaje saikuma ahankali yadan yunkura yana tunanin maganan Mami "this is a second chance Allah yabaka Zayn" bude kofar motan nashi yayi ahankali yasauko dasauri bodyguards dinshi suka tsaya agabanshi, wani kalan daura hannu yayi agoshinshi cikeda takaici yace "for f**k sake i wanna go to the mosque" kallonshi duka bodyguards din sukayi cikeda mamaki, dan gajeren tsaki yaja ya bangajesu yawuce mosque abinshi suka bishi dayake su arna ne gaban masallacin suka tsaya kaman an bishiyoyi suna jiranshi.

Shigowa dakin Mami tayi wajajen zuhur ganinta tana bacci kan kujera rikeda wayan Zayn yasa tadan ware idanu, Zayn haryasoma jin maganan tane wanan daya bama yarinyar wayanshi tarikemai does that mean yama yarinyar godiya, dan murmushi tayi takaraso ciki basuda wani kaya hakan yasa kawai after dress daya sayama Farrah tadauko tazo inda take tabata tayi tace "Farrah Farrah" gently tabude idanunta takalli Mami, murmushi Mami tayi tace "tashi mutafi gida kinji" gyadama Mami kai tayi sanan tamike tsaye ahankali, abayan ta warware da taimakon Mami ta iya daga hannu Mami tasa mata ta makala boturan sanan takai hannunta ta gyaramata hulan dake kanta daya zamiye baya tana kallon gashinta Mami tace "kikaji sauki sosai zan kaiki saloon a gyara gashin nan ko" ahankali tace "to" ita kanta saida tai mamaki datai magana this time bai breaking ba Mami ma murmushi tayi tace "masha Allah, Beautiful Farrah is talking now, muryanki dadi Alhamdulilah" handbag dinta Mami tadauka bayan tahada komi nata ciki sanan tabama Farrah wayan Zayn tace "rikemai wayanshi mukaje sai kibashi" karban wayan tayi sanan suka fito tareda Mami ahankali take tafiya sai kallonsu ake, duk Dr dazaisa Mami saiyace "is she your daughter Mrs Ganuwa she's so Preety" murmushi Mami take tana cemusu yes, waje suka fita suna tafiya zuwa parking space daidai shima Zayn nafitowa daga masallaci, kallo daya Mami tamai tadauke kai amman ba karamin Dadi taji ba, hanyar motanta tayi dake kusada motan Zayn, takalli Farrah dake tsaye kusada ita tace "ba Zayn wayanshi kizo muje" Mami tai maganan tana shiga bayan motan, ahankali Farrah tajuya, ganin Zayn harya shiga bayan tashi motar yazauna yasa takarasa wajen ahankali tadaure fuska dan bata manta stupid din daya kirata dazu ba, ganinta tsaye gaban motanshi yasa yadan kalleta kaman baiso yakalleta, daure fuskanta tayi tamau sanan tamikamai wayanshi dake hannunta, kallon hannunta yayi dake rikeda wayanshi sanan yadan kara kallon fuskanta, ganin kallonshi take still fuskanta adaure yasa ahankali kaman baiso yakai hannunshi zai karbi wayan, haryasa hannunshi kan wayan zai zare daga hannunta tawani fizge wayan ta nakamai wayan akan kujera sanan ta watsamai harara a idanu tajuya fuuuuuu tawuce tashiga motansu bodyguard din Mami yarufe motan yakoma gaba yana tada motan Mami kuma hankalinta nakan wayan datakeyi.
Tsayawa chak Zayn yayi da hannunshi dakenan a position din dayake na karban wayan sanan

yakalli wayan data ijiyemai kan kujera, wani kalan zafi yaji aranshi daya kasa daurewa yadanyi giggling cikeda mamaki yace “Wowww!” Bodyguard dinshi dake tsaye gaban motan ya kalla sanan yanuna kanshi yace “did you see what that village little gurl did just now?” Saukar da kanshi kasa bodyguard din yayi dasauri, cikin fushi Zayn kaman bodyguard dinne yamai laifi yace “shut the door get into the damn car and drive me home motherfucker!” Ya dannamai rude rich kids zagin nan kirjinshi na tafarfasa.

“Just tell me what exactly kikeso nayi? Eh” cikin tsantsan masifa tace “you are the root of this whole mess damuka shiga, inda ka yarda muka bama Oga order akashe dan iskan yaron nan da tuni yatashi aiki” wani kalan dan dariya Uncle yayi more of dariyan dazaka kira da dariyan takaici, saida yayishi ya koshi sanan yadago idanunshi dasukai jajir yace “tayaya zan taba bada order akashemin nephew? How do you guys even think zan iya haka for god sake dandan yayana wanda nake uwa daya Uba daya dashi how?!” Yay ihu, wani kalan mugun tsaki Hajiya Fatima taja, Hajiya Mariya da takaici yagama kasheta tace “thank you Fatima da wanan tsakin, wlh ko kadan bakasan ciwon kanka ba, kace nephew? Nephew din dabaisan darajan kaba, baisan amfanin ka ba all u are to him is dan boyi boyi” wani yunkurowa Uncle yayi daga kan kujeran dayake zaune kaman zai mari Hajiya Mariya, Hajiya Fatima tace “dukanta zakayi, yo karya tamaka, kai har kanada bakin kace dandan yayanka uwa daya Uba daya, to wlh bari kaji in fadamaka indai har aka ake yaya aduniya to Allah karya bani irin yayanka na yamaida ni dan aike, ta yanda zakasan ko tunanin ka bama yayi yatashi gabaki dayan dukiyan shi yabawa danshi batare daya baka ko kwabo ba” baki Hajiya Mariya tabude zatai magana Uncle da idanunshi sukai jajir yabuga table tareda daka musu tsawa yace “enough! We are here to discuss solution idan lecturing dina zakuyi ne sai kuyi kugaji, ni abinda nakeso kudin Yaya nakeso gabaki dayanshi, wanda nake gani idan nasamu zan iya rabamana shi gida uku, kowa yadauki daya, inda kun yarda ahakan na tabbatar da mutanen nan da tuni sunsa Yaya yarubuta komi yabasu takardan in exchange ma rayuwan Zayn babu abinda bazai iyayi akan Zayn ba, amman ku kukaki ku duka biyun kukeso akashe Zayn sanan akarbe kudi, yanzu dai kunsan an kama Lamba ko, luckily for us Oga yay assuring nawa baisan komi kan mu da muka basu kwangilan ba, so kozai fadi wani abu idan yaji azaba saidai kansu bamuba, so for now asirin mu arufe, he’s demanding abashi kudin aikin shi koya fasa kwai, sai magana tabiyu what’s the way forward yanzu kowani security na gida da waje Yaya yayi doubling komi, tayaya zamu cimma burin mu” jaka Hajiya Mariya tabude taciro wasu bandir bandir na 100 dollars ta ijiye guda biyar kan table tace “nidai ga payment dina, banda wata matsala data wuce Zayn, nasan kudi baya isan mutum aduniya mukaci nasara muka sami kudin Alhaji inaso, amman Zayn dai sainaga bayan yaron nan aduniya, duk sanda na ganshi nakanji wani abu ya tsayamin awuya na bakin tsanan shi uwa na lumamishi wuka aciki ya mutu nakeji, I think the easiest way dazan iya kashe yaron nan is da taimakon diya mace tunda shi Allah yayishi bunsuru ne” wani dan murmushi Uncle yayi yace “aikam kinada aiki, Zayn abaiban mutum ne dazakiyi shekaru aru aru baki gane kanshi ba, miskilin mutum ne na karshe, haryau banga wacce Zayn yakeso aduniyan nan ba, kowace mace yasamu kawai kawad da sha’awan shi yakeyi da ita yabarta anan, I believe ki chanza plan” wani kalan murmushi Hajiya Mariya tayi sanan takalli Hajiya Fatima tace “kin tuna

Layla Fatima”? Wani kalan makirin murmushi Hajiya Fatima tayi tace “natuna ta” Uncle dabai gane me ake cewa ba yace “waye kuma Layla”? Murmushi sosai Hajiya Mariya tayi ta gyara zama tareda wani kalan juya kujeran datake kai tace “let’s just say Layla is a girl I picked on from the street lokacin iyayenta na kangin talauci, infact irin buzayen nan ne dasuka zo from chadi, suna bara kan titi, long story short I sponsored education nata a England ta karanta Mass com, yanzu haka tadawo nasan tanama gida tana jirana, iyayenta sun mutu I am morethan iyaye awajenta, bantaba ganin yarinya mai kyau kaman ita ba, kowaye Zayn yayi kadan yay resisting yarinyar nan, I will use her to get to throat din Zayn” tabe baki Uncle yayi yace “good luck with that” yasa hannunshi ya tattaro kudaden da Hajiya Mariya ta daura akan table din yace “bani kudin ki Hajiya Fatima” itama same amount da Hajiya Mariya ta ijiye ta ijiye Uncle ya tattara ya kwashe ajaka sanan yatashi yana rataye jakan yace “good luck Ladies, do your path while I do mine” yawuce yafita daga dakin, juyowa Hajiya Fatima tayi tace “are you sure Layla zata iya aikin nan karyazo instead of tasamo miki throat na Zayn, Zayn ne zai sami throat nata you know what I mean just look at Zayn, yaron nan yahadu my god, ga kyau ga gayu ga body da mata keso ga shagwaba” wani kalan murmushi Hajiya tayi tace “bakisan waye Layla ba saisa kike magana haka” dariya suka dan yi, Hajiya Mariya tace “I want to see Mami tai kuka na bakin ciki kaman yanda ta kwacemin miji na, i want her to suffer tai experiencing pains danayi arayuwan nan ta dalilinta, kiri kiri yanzu idan Zayn na bukatan Alhaji zai hakura da Kwanan mu yaje wajen danshi, muyi kishi da Zayn muyi kishi da uwarshi, jiya adakina yake amman sabida wanan wayward son of his na tsoro ya kubuta yaje ya kwana dashi, I hate hate extremely hate that drug addict yaron nan nashi” tabe baki Hajiya Fatima tayi tace “ni wlh da Allah yabani d’a irin Zayn gwara ma na mutum nan haihu ba, babu kalan kwayan dabaya sha, tun kafin ya balaga Nany shi nakeji take gayama ubanshi takama shi da mace, yaro haka har abin sone” “saisa nake addu’a Allah ubangiji karya shiryashi yakare haka a wulakance ja’irin yaro, tashi kiwuce kafin nima nafito yanzun nan kada aga duk mun dawo thesame time, ni tausayi ma amaryan shi Mariya kebani” ta kwashe da dariya tace “tunda Zayn yadawo billahillazi Alhaji baimasan yanada wata Amarya ba” tashi Fatima tayi tace “shag ya manta da ita, kinji Bari na wuce saikin shigo kema” key motarta tadauka tana tabe baki tace “mu sauran matanshi mune bamu da bodyguard, Maman dan iskan danshi tanada shi hakama danshi” dan dariya Hajiya tayi tace “karki damu komi yazo karshe” wucewa Hajiya Fatima tayi tafice wata arniyan mota tashiga taja tabar gidan dasuke ciki wanda yake karamin sabon gida, almost one hoOur sanan itama HajJiya Mariya tafito tashiga tata motar tabar gidan.

EPISODE1️⃣8️⃣

Parking tayi abangarenta tafito, wata doguwan kyakkyawan budurwa ce tafito daga babban flat dinta, fara ce ita kal yarinyar tana sanye da jeans da riga babu dan kwali akanta tayi kitso da aka kara da attachment kalan blond daya sauko har waist nata, tana zuwa batai wata wata ba ta rungume Hajiya Mariya tace “oyoyooo Mommy” rungumeta back hajiyan tayi tace “oyoyo my baby girl, my Lailarosh, how are you”? Murmushi tayi tabude baki zatai magana aka bude gate din gidan, kallo daya Hajiya tama motar Mami tadauke kai tacigaba da kallon Layla tace “how was your flight”? Murmushi tayi tace “fine” daidai motan Mami yay parking kusada na Hajiya

saukowa bodyguard yayi yazo dasauri yabude ma Mami kofa tafito Farrah ma na fitowa, daidai lokacin kuma motan Zayn ya dannokai cikin gidan shima, ganin Hajiya Mariya yasa Mami data kama hannun Farrah wacce daga Hajiya har Layla kallonta suke tace “Hajiya barka da rana” murmushi Hajiya ta kakalo tace “Barkan mu dai Mami ya Zayn da jiki hope bai makance ba” dan murmushi Mami tayi tace “Alhamdulillah komi yazo dasauki” kallo Hajiya tabi Farrah dashi tace “wanan kuma fa daga ina” tama Farrah wani kallon wulakanci, Farrah Mami takalla tana murmushi tace “itace Farrah, yarinyar data taimaki Zayn, she is going to stay damu for now, she don’t speak hakanan” jan Farrah Mami tayi ajikinta cikeda so tace “Farrah gaida Hajiya” ahankali Farrah kanta akasa dan batasan mesaba batason kallon da Hajiya kemata tace “i……i….ina…….yi…ni” Zayn da fitowanshi daga motanshi kenan dan satan kallon Farrah yayi dayaji tai magana da kyar baisan mesa ba but har cikin zuciyanshi yaji muryan nata, dauke kai yayi batare daya kara kallonsu ba yawuce zaije side nashi kaman jira Hajiya Mariya take tace “Zayn ga friend namaka her name is Layla” wani kalan juyowa yayi yakalli Hajiya yatsine fuska yayi irin nagayamiki I need friend ne sanan yajuya cikeda bacin rai zai wuce, da kakkausan murya Mami tace “Zayn” chak ya tsaya sanan yajuyo ahankali sai alokacin yadan kalli Layla dake kallonshi kaman zata cinyeshi batare dayay magana ba, dasauri hajiya ta tabata tace “bazaki gaida yayanki ba” murmushi Layla tayi cikeda siyasa tace “Hello Zayn” adikile yace “Hey” sanan yajuya yawuce, murmushi Hajiya tayi tace “itace diyar kanina daya rasu yabari shes 21 tagama school a england” kallonta Mami tayi kana ganin Layla kasan tafi 21, kabata 25/26 dan zata iya zama mate din Zayn kawai Zayn yafita girman jiki ne, dan murmushi Mami tayi tace “bari nakai mara lafiya ciki” takalli Layla cikeda wasa tace “sai kinzo tayani hira” sanan takama Farrah dakebin gidan da kallo tawuce side dinsu.

Side dinsu suka shiga wanan karan Mami saida tai dariyan yanda Farrah ke kallon komi kamata tayi sukai sama tace “muje nakaiki dakin ki saiki wanka, za’a kawomiki abinci, kika gama zanzo nabaki magani da allura, kome kikeso kifada min zan sa amiki, ki dauki gidan nan kaman gidanku sanan kidauke ni kaman mahaifiyar ki ki saki jikinki kinji” sukai maganan daidai suna shiga wani lafiyayyen daki mai bala’in kyau kan gado takai Farrah tace “nan ne dakin ki, ga bayi nan” Mami ta nuna mata bayin, sanan tanuna mata wardrobe tace “kowani kalan kaya kikeso kisa yana nan, yau dasafe nasa aka sayo kaya aka sassaka miki aciki, bari naje nabaki wuri ko, kiyi sauri ki gama kisha magani” Mami tai maganan tana juyawa zata fita, wani abu Farrah taji ya tsayamata awuya, ahankali tashiga bude bakinta dake wani kalan rawa yana shaking murya chan kasa sosai tace “Maaaami” for the first time Mami taji muryan Farrah yadaki zuciyanta dawani kalan sauri Mami tajuyo, hawaye taga Farrah tasa hannu tashare daga kan fuskanta sanan ahankali tamike daga kan gadon, dawani kalan sauri tazo wajen Mami batai wata wata ba tawani fada jikin Mami sai kuka, sosai take kuka har saida Mami ta tsorata tace “Subhanallahi Farrah menene kike kuka haka” kankameta Farrah tayi tana kuka sosai, fuskanta na jikinta ahankali tace “Mami naa…….gode” hawaye Mami taji sunzo mata idanu dasauri ta hadiye hawayen taciro Farrah daga jikinta, hararan fuskan Farrah tayi sanan tasa hannunta ta goge hawayen dasuka jika mata fuska, bawasa kan fuskanta tace “koda wasa kada ki kara cemin kin gode Farrah ni Maman kice, badan sabida ki taimaki Zayn nake all this ba, hakanan ko Allah yaga zuciyata kawai ina sonki Farrah, I look at you kaman baby girl dana dade nake

kwadayi Allah yabani finally yakawomin ke, sOo yanzu imaza maza kiyi wanka" Mami tai maganan tana kama hannunta zuwa bayJi, kunna mata ruwa tayi sanan tafice.

19

Tsaf tayi wanka dan tanada karfin hali, tariga tasaba duk dukkan daza'amata dole tai aiki, fitowa tayi daga bayin ta shirya, dadduman dataga an shimfida mata yana kallon gabas tahau ta tafara salla addu'a tayi cikin salla kan Allah ya zaba mata abinda yami mata alkhairi arayuwanta.

Wuraren 4 na yamma Alhaji yashigo gidan, ana budemai mota ya sauko daga motan yana gyara zaman babban rigan dake jikinshi, direct side din Zayn yawuce bodyguards dake tsare gaban side din Dad yakalla tareda amsa gaisuwansu sanan yashiga flat din Zayn dake wani kalan lafiyayen kamshi ga sanyin AC tako'ina daidai lokacin kuma Zayn dake sanye da bathrobe fari yadaure igiyan agaban rigan kafanshi sanye da bathroom slippers yafito daga kitchen dinshi da glass of milk a hannunshi yana kurba dasauri Alhaji yace "why are you getting milk dakanka bayan kanada masu maka"? Dan yatsine fuska yayi yana shigowa cikin falon, kan kujera yazauna tareda daura kafanshi daya kan dayan ahankali yace "I want to start doing everything myself from now, daga yanzu su daina shigomin cikin daki su tsaya nan bakin kofa" dan murmushi Alhaji yayi yana kallonshi trying to read something yace "ohh that's new" zama yayi kusada Zayn din yana kallon farin glasses din da akamai na hospital dayake sanye dashi shi, glass din yamai kyau ba kadan ba, baki yabude zaiyi magana Zayn yarigashi ahankali yace "Papa" yay maganan yana ijiye glass na milk din kan coffee table sanan yadago, ahankali Alhaji daya tattaro duka natsuwanshi yace "Na'am Zayn menene me kakeso"? Dan juyowa Zayn yayi yakalli Baban nashi kallon daya dade baimaiba murya chan kasa yace "Dad am I being immature"? Yanayin fuskanshi kadai Dad yagani yagane he's serious da tambayan baki yabude zaiyi magana cikin yanayi na baison yamai karya Zayn yace "don't you dare lie to me Dad kafada min gaskiya please, I don't have anybody, you are my best friend Dad, am I being immature"? Tsayawa Alhaji yayi yana kallon Zayn kalman best friend daya kirashi dashi wanda Zayn baitaba kiranshi dashiba yasa yaji kaman yay kuka, gently ya gyadama Zayn kai yace "yes! But just a little Son, I guess u just 26 still a kid that's why" girgiza kai Zayn yayi tareda dan juya idanu irin na sangartattun yaran nan yace "no Dad, I think I am being incentive Dad, I am selfish and extremely rude" dasauri Dad yace "noooo Zayn kada ka kara kiran kanka haka, Zayn you are one sweet Human da duk wanda zai zauna dakai saiya soka, you are just being yourself, chasing your likes abubuwan dakakeso, and you are one reserve person baka shiga rayuwan kowa, shiru shiru, you are just the way you are, and being the way one is doesn't mean he's rude or incentive or even selfish, you are Zayn, my only son, abin alfaharina, kyautan da Allah yamin" yay maganan yana kama hannunshi mai lafiya trying to assure him abinda yafadamai gaskiya ne, shiru Zayn yayi yana kallon Babban shi na kusan 2min kaman yanda Baban nashi ke kallonshi, ahankali yace "Dad" ahankali shima Alhaji yace "na'am Zayn dina meke damunka haka nafara shiga damuwa wlh, menene talk to me, kome kakeso consider it done" dan ijiyan zuciya Zayn yasauke sanan yakalli hannunshi dake nan adaure yana kallon igiyoyin dan kwallin Farrah data dauremai hannunshi dashi, yatsanshi yakai kan igiyan yana

tabawa murya chan kasa kaman mai tunani yace “When those goons kidnapped me Dad I went through a whole lot, I lost all hopes, was thirsty, hungry, ga karaya ga idanuna ga lot of spiders Dad at that point everything was a thing for me, I looked up to the sky nace Allah ya taimaken, then that gurl came from nowhere kaman daga sama aka jefota” yadanyi shiru yana kallon hannun nashi still in a very very low tone yace “Dad that girl protected me with all she got, at first I thought she was an angel, Dad kasan dan kwalinta tayaga ta dauremin hannun nan” yay maganan ahankali yana shafa hannunshi saikuma yadan yatsine fuska ahankali yace “Dad kasan I couldn’t thank her, whenever I looked at her sainaji she’s too small nace mata thank you and I am not use to thanking anybody” yadanyi maganan yana murmushi iya lebe kafin ahankali yace “Dad jikina is telling me I need to do morethan a thank you, she saved my life nima I should save her life and even give her a better life, education, da sauransu, Dad ina Uncle dinta kasa an daukoshi?” Dad na kallonshi right in the eye ya gyadamai kai, ahankali yace “tun around 3 chopper su yasauka, suna biyeda ni maybe ma yanzu haka sun shigo gidan nan” shiru Zayn yayi yana kallon mahaifinshi, lips dinshi ne yashiga rawa kaman yana fighting da abinda yakeso yafadi dan lumshe idanu yayi sanan yabude su yadaura su kan Dad ahankali yace “Dad can you adopt the girl please?”! Shi kanshi Alhaji saida yakara kallon Zayn maganan tazomai wani bagtatan bawai adopting yarinyar ne matsalan shiba ko kadan but this is the first time in history Zayn yacemai please kan wani abu mamaki ma hanashi magana yayi, ahankali Zayn yakai hannunshi yadaura kan na Alhaji yace “Dad lokacin da Mami tace the girl has been abused I felt so so guilty, bansan anything akanta ba but I know batada iyaye, and I know her uncle ran away they don’t like the girl, she’s like a burden, let’s call our lawyer muyi adopting nata idan ma so suke mukara musu wani kudi zamu kara, Dad I want to sponsor her education with my money not your own just to repay her kaji Dad” yakarashe maganan yana jijjiga hannun Alhaji, wani kalan sassanyar ajiyan zuciya Alhaji yasauke yana kallon fuskan Zayn din sanan yace “duk wanda cannot see beyond this your face da ake gani kaman u are rude is blind cus this your heart” Alhaji yakai hannunshi kan kirjin Zayn yace “is made from gold” dan murmushi Zayn yasaki, dan hararanshi Alhaji yayi yace “what are you waiting for, jeka saka kaya karakani nayi adopting yarinya ta Farrah” dan murmushi Zayn yayi yatashi glass cup nashi yafara dauka ya shanye milk din ciki sanan yawuce sama bai wani dade ba wani dark blue hoodie yasaka da gajeren wando iya gwuiwa milk, ya sanya eye glasses dinshi sanan ya feffesa turare yafito kafafunshi sanye cikin wasu navy blue designers crocs simple kayan zZama gida but still ka kalleshi saika kara kalloOnshi suka fito daga side din Zayn din tare.

20

Side din Mami suka wuce, Mami na zaune a falo tana magana da Mama awaya suka shigo ganinsu tare yasa ta hararesu tacigaba da wayanta zama kusada Mami Alhaji yayi yana kallonta sabida tai kyau taci gayu sosai cikin kace kai kyau, katse wayan tayi takalleshi tace “ne kake kallona haka” cikeda tsokana yace “wai ke baki tsufa ne jibeki saikace ba kene kika haifi wannan gansamemen saurayin ba” yanuna Zayn, dan dariya Mami tayi tace “I take that as a compliment” “ina Farrah”? Alhaji ya tambayeta anatse, murmushi tayi tace “tana sama nabarta cartoon take kallo a IPad dina, you need to see yanda maganan ta ke improving Alhaji, one thing I like about her is she is fearless tanada kwazo da jajircewa” murmushi Alhaji yayi yace

“kiramin ita” tashi Mami tayi tai sama bata wani jimaba suka shiga saukowa tareda Farrah, tana sanye da doguwan riga na atampa brown dinkin yamata das das ajiki sai dan kwalinshi data daura aka kanta na kasa wani kunya taji tanaji ita Mami tafiso da Mami kawai tasaki jiki saukowa kasa sukayi Mami ta zaunar da ita kan kujera kusada ita kasa zama tayi tazame jikinta ta zauna akasa da sauri kanta na kasa tashiga wasa da yatsunta Dan dariyan manya Alhaji yayi yace “Farrah yaya jikin? Wajen dinkin yadaina zafi”? Gyadama Alhaji kai tayi ahankali cikin zazzakan muryanta tace “eh…..Ab….ba”  jinjina kai Alhaji yayi yana murmushi yace “Masha Allah, ga muryanki nan Tubarkallah Allah kara sauki” “Farrah” yasake kiranta anatse hakan yasa ahankali tadago kanta ta kalleshi, ajiyan zuciya Alhaji yasaki, yace “kingan ni nine mahaifin Zayn, mijin Mamin ku, da Mariya da Fatima da Maryam, Zayn kadai Allah yabani, rana daya kuma Allah yakawoki cikin rayuwan mu, akwai abinda yasa nasaka aka kiraki, inaso na tambayeki ne naji amsanki kafin nai komi” yasakeyin shiru sanan ahankali yace “Farrah kawunki ya sanar damu ke marainya ce, matata nan Maman Zayn likita ce, itace tamiki aiki a operation, taga tabo da dama ajikinki wanda yake nuna na alamun duka ne, yanzu inaso namiki wani tambaya banso kimin karya kinji” gyadama Alhaji kai tayi ahankali, anatse Alhaji yace “wanene yasamiki garwashin wuta abaki?” Shiru tayi gabanta nafaduwa dum dum, dafata Mami tayi ahankali tace “kada kiji tsoro ki yayi gaskiya kinji” gyadama Mami kai tayi sanan takalli Dad, batasan ya akayiba kasa karya tayi ahankali tace “In…na” “Matar kawunki”? Gyadama Alhaji kai tayi tace “eh””ita ke dukanki ma”? Gyadama Alhaji kai tayi takai bayan hannunta dasauri tashare hawayen daya zubomata, shiru dakin yayi Alhaji na kallonta, murya chan kasa yace “akwai abinda ake cema adoption aturence, yana nufin zaki dawo diyata ni da Mami da kotu tabamu mune custodian naki, kula dake yafita daga hannun su kawunki yadawo hannunmu dundundun ki dawo yarmu musaki amakaranta da sauran su, nakira lawyer na halama ya iso yanzu, yanzu hakama kawunki da matarshi na gidan nan chan bangaren baki, amman so naki nafara jin bakin ki kafin nasa akawo kowa nan, Farrah” Alhaji yakirata ahankali murya chan kasa tace “Na’am” ahankali yace “kin yarda ni da Mami muzama iyayenki?” Wasu kalan hawaye ne suka cika idanunta, tunda take baa taba bata daraja da mahimmaci dahar za’a zaunar da ita atamabayi yardanta Awani abu ba sai yau, tunda tahadu da mutanen nan sunada kirki sosai, batada kowa aduniyan nan banda kawu shi kadai gareta amman shima baya sonta baya kaunarta agabanshi aka kashe mata yar uwa baice komiba, dafata Mami tayi dasauri ta kalli Mami, Gyadamata kai Mami tayi alamun tace “eh” ahankali tace “eh Abba” rungumeta Mami tayi tana share mata fuska tace “daina kuka to” sai alokacin Zayn yadan saci kallonta, fuskanta na jikin Mami tana goge hawayen dasuka zubomata kaman ance ta kalleshi hada idanu sukayi da Zayn din hararanshi tayi tareda dauke kai.

Dauke kai shima Zayn yayi dasauri yana regretting kallonta ma dayayi waya Alhaji yayi sanan ya katse wayan yakalli Mami yace “tafi da ita sama”.

Wani Babban lawyer Alhaji ne yashigo falon tareda Uncle, sai Malam da idanunshi sukai zuru zuru da Inna da itama idanunta sukai zuru zuru, Malam yay mamaki dahar gida aka shigo aka

daukesu suka shiga jirgi, Inna ihu tadingayi a helicopter wai zata mutu hanjin cikinta zasu zube.

Malam na ganin Alhaji da gudu yataho gabanshi ya tsugunna yahade hannayenshi biyu yace “Alhaji dan girman Allah kayakuri kada ka karbe kudaden daka bani, wlh wlh shairin shaidan yasa na gudu nakoma kauyenmu, to inbama shairin shedan ba ai nasan Kunsan kauyen kuma nakama nagudu, Alhaji dan Allah kayakuri wlh bazaka gane bane, Alhaji nima diyata daya rak, ina fama dakai na, kanwata tazo ciwon datayi shine ya tsiyatar dani tatas banda ko kwandala matata ce keda awakai suma awakan ranan da Farrah ta ceto dan gidan ka duka ta batar dasu, wlh ashirmena naso nagudu ne kawai nahuta inje na karata da matata da diyata guda amman nai kuskure kuya kuri” tunda yake maganan kowa ke kallonshi, cikin fushi Uncle yace “ina miliyan goman damuka baka bamu kayanmu ku dauki yarku amaidaku kauyenk……” tsayar da maganan datakeyi yayi ganin Alhaji yadagamai hannu, nuna kanshi Alhaji yayi yace “kai tun kana dan kankanin ka kataba ganin nai kyauta sanan nadawo na amshe kyautan danayi” sunnar da kanshi kasa Uncle yayi yace “a’a Yaya” maida hankalinshi kan Malam Alhaji yayi da Inna da itama ke zube gaban mijinta jikinta na rawa tunda take bata taba ganin aljannan duniya irin gidan nan ba, murmushi Alhaji yasakin musu yace “ku zauna da kyau dan Allah ni bakamin komi ba kuma bansa adaukoka sabida kudin danabaka ba nariga nabaka gonakin suma nariga nasa anma mai garin ku magana shi gwamnan Adamawa duk sanda ka koma zaka amsa koba komi yarinyar da bakaso yarinyar daka gudu a asibiti kabarta kaga kaci arzikinta” Alhaji yakara murmushi jikin Malam yay sanyi yakoma ahankali ya zauna hakama Inna, gyaran murya Alhaji yayi yace “abinda yasa na nasa akawomin kai nauyin dake kanka kake kokarin gudun mawa nakeso nacire maka shi daga kanka gabaki daya, diyarku Farrah nakeso nazama mahaifinta a shar’ance, cinta shanta, suturanta karatunta duka yadawo kaina, zai zamto Farrah tadawo diyata shine kawai abinda yasa na nemoka zaka bani”? Alhaji ya tambayeshi dasauri Malam jikinshi har bari yake yace “eh eh wlh nabaka Alhaji” Inna ma dan sosa keya tayi azuciyanta tanaji inama ace Rakiya ce ta taimaki yaron, kaman ta chakama kanta wukan bakin ciki takeji, kallon Lawyer Alhaji yayi yace “give him the papers” tashi yayi zuwa wajen Malam dan yabashi papers din yakuma nunamai inda zaiyi signing, dan yatsine fuska Zayn yayi yamike tsaye hanyar stairs yayi yay sama abinshi, shi kanshi baisan mesa yazo saman ba kujeran dakenan falon sama ya zauna yana kallon kofan dakin da yake tunani nan ne dakin Farrah dan shine dakin dake kusada na Mami, yadade yana kallon kofan, kaman akwai abinda ke controlling nashi tashi yayi zuwa gaban dakin yay jimmm yana kallon kofan, ahankali yadaga hannunshi yakai zaiyi knocking kofan dan cizan lips dinshi yayi yasauke hannun kasa ahankali, sake daga hannun yayi zaiyi knocking daidai nan aka bude kofan Farrah ce tabude kofan da saurinta dan ana kiran IPad din Mami dake wajenta zata kaimata saura kadan tafada jikin Zayn ta tare kanta ta hanyar kai hannunta daya ta daura kan kirjinshi daidai saitin zZuciyanshi as kariya daidai loOkacin kirjinshi ya buga dumm!

21

Yanda taji bugawan kirjinshi a hannunta da sauri ta janye hannun daga kan kirjinshi hannun nata nadan rawa, dauke kai yayi dasauri daga kallonta kaman ance dole yay magana yace “on

Monday zan kaiki school ki shirya" yana maganan yajuya da sauri yawuce itama juyawa tayi takoma dakinta da wayan batasan mesa ma gabanta ke faduwa taganshi ba ya chanza mata a idanu gabaki daya kaman bashine mutumin daya bata tausayi ranan dataga za'a kasheshi ba.

Zama yayi ahankali a dinning Mami tace “when was the last time kaci tuwon shinkafa”? Dan kallon fuskan Mami yayi yace “I can’t remember” zubamai Mami tayi da lafiyayen miyan busashen kubewa yaji kifi tasamai spoon dan tasan bazaici da hannu ba, sanan tawuce takoma wajen Dad tacigaba da yankemai kumban, saukowa Farrah tayi bayan ta chanza kayan makaranta tasa wani Riga da skirt na kanta black and white dasuka mata kyau ko dankwali bata daura ba ko kadan batasan Zayn na dinning ba falo ta sauko kaman zatai kuka tace “Mami yunwa” Mami dake yankema Dad kumba tace “jeki zuba yana dinning” juyawa tayi zatai dinning Zayn tagani zaune yana cin abinci, daure fuska tayi tawuce dinning din ko kallonshi batayiba shima haka ta dauki plate ta saka tuwo tazuba miya da namomi daban daban sanan ta zauna adayan side of the dinning tafara ci Zayn yadan saci kallonta namomin dayagani tazuba saida yasa yakusan tuntsirewa da dariya, ijiye spoon din yayi bayan yaci just little dan shi he’s not a of su tuwo sanan yamike yana rike da glass cup na juice kaman zai zaga ya ijiye wani abu yana zuwa ta bayan Farrah bata ankaraba kawai hannunshi tagani cikin plate na abincin ta ya kwashi namomi iya naman da hannunshi suka iya kwasa dabaisan guda nawa bane, zabura tayi ta mike tareda kwala kara, tace “Mami, Mami kinga Ya Zayn ya debe mini namomi na ko”? Dasauri Zayn yatura namomin abakinshi daidai Mami da Dad najuyowa suka kallosu wani kalan kwarewa Zayn yayi dayasa yafara tari ya watso namomin waje Farrah tahau dariya sosai, Dad yataho wajen harda gudu yakama Zayn din yana bubbugamai baya yace “sorry son, bani ruwa Farrah” ruwan ta tadauka tabama Dad, Dad yakarbi ruwan zaikai bakin Zayn dasauri Zayn yature ruwan yace “bazan sha ruwanta ba Dad” dariya sosai Farrah tayi harda tsalle tamai gwalo tace “eh nima banso kashamin ruwa kasha naka” tsayawa daga Mami har Dad sukayi suna kallonsu juice dinshi Zayn ya kwankwade tass sanan tarin ya tsaya, yakalli Dad yace “Dad kar akara bari tana kwasan nama haka, all she knows how to do is cin abinci babu abinda ta iya” murgudamai baki Farrah tayi yajuya yafice daga dakin fuuuu.

Dad yakalli Farrah dake tsaye har lokacin tana murmushi yace “cinye abincin to azo agyara wajen” gyadama Dad kai tayi dasauri tazauna tace “Dad ni zan gyara dazaran nagama ci, na iya ai ko Mami” Gyadamata kai Mami tayi, Dad yadawo ya zauna, mota Zayn yashiga yafice harzai wuce masallacin su nawaje sai kawai yatuna baiyi salla ba, dan yatsine fuska yayi zagin Farrah na fadomai arai takirashi stupid irresponsible boy&, zai nuna mata he’s responsible kuma yasan abinda yakeyi.

45

Wuraren 10 aka budema Uncle gate yashigo gidan yana kallon ko’ina he can’t wait for lokacin

da all this money will be his, saiya gina gidan dayafi wannan kyau yay alkawari, bari Yaya yayama zaman gidan da akasa yayi a asibiti yahuta yadawo office zaisa yakira lawyer shi, anyway mema yasa yacemai yazo da sassafen nan haka.
Wuraren 10 Uncle yashigo falon Mami, tana zaune ita kadai tana duba wani medical book hakanan ga farin glasses a idanunta, gaisawa sukai da Uncle dake sanye da manyan kaya yace "Mami ina Yaya"? Sama Mami ta nunamai tace "yana dakinshi asama" daidai lokacin Dad yahau saukowa daga stairs yaci manyan kaya farare yana kamshi, kallonshi Mami tayi tace "I thought you are still on bed rest ina kuma zaka"? Wani kalan murmushi yayi yazauna kusada ita yace "I will tell you about it idan nadawo yanzu baga Uncle din danki ba he will take care of me don't worry" kallonshi Mami tayi kaman zatai magana saikuma tai shiru, tashi Dad yayi hakan yasa Uncle shima yatashi yadubi Mami yace "tom saimun dawo" "adawo lafiya" dukowa Dad yayi ya manna mata peck a goshi yace "smile for me Matata" dan murmushi tamai hakan yasa yace "tom natafi, idan Zayn yadawo daga wajen aiki kice nace kada yafita yajirani" gyadamaikai tayi tana kallonshi yafice daga dakin.

Saida suka shige jeep din Dad bodyguards suka rufo kofan sanan Uncle yadubi fuskan Dad yace "Yaya wai ina zaka ka kirani karfe biyun dare kaga yanda naji tsoro nazaci wani abu yama sameka ne, ance kadinga bacci maisawai baka iya bacci, me kake tunani haka"? Dan ijiyan zuciya yasauke ahankali yace "tunanin Zayn kehanani bacci" yadaga kanshi yana kallon bodyguards dinshi dake tuki ahankali yace "when we get on board we will talk about it" gyadamai kai Uncle yayi haka dukansu suka zauna sukai jugum har airport, wannan karan private jet suka shiga saida suka tashi sanan Uncle yakalli Dad dayay nisa atunani yace "Yaya wai ina zamune? Yaya tell me what is going on, wani abu yakuma faruwa ne ko Zayn yamaka wani abune Dan Zayn ne kadai kesa kashiga irin wannan damuwan aduniya" dan ijiyan zuciya Dad yasauke ahankali ya kalli Uncle yace "nayi magana da governor Adamawa yanzu haka motoci na jiranmu a airport dashi gwamnann inaso naje kauyen nan na nemama Zayn auren Farrah, inaso adaura Auren!" Wani kalan kallonshi Uncle yayi gabanshi na bugawa ahankali yace "did Zayn know about this?!" Girgixamai kai Dad yayi yace "hatta mahaifiyar shi batasani ba dan banson any abu dazai batamin hukuncin dana yanke bayan angama komi nakoma gida zan gayamusu" daga Uncle har Dad din shiru sukayi suna kallon juna, murya chan kasa Uncle yace "Yaya kasan aure baya gaban Zayn, banda haka ayanda Zayn yake tayaya zai iya rike Farrah amatsayin mata, bama wannan ba kanaganin Zayn zaiso Farrah she is just 18, Yaya anya wanan decision din naka is right kuwa?" Shiru Dad yayi kafin ya sauke ijiyan zuciya yakalli Uncle yace "bayan abinda yasameni dan zaman gidan nan danayi na hutu I was seriously praying har istikhara nayi kan Zayn bawai hakanan natashi zan hada aurensu ba naga abubuwa da dama na sign da alamomi da Allah ya nuna mini dayasa na natsu da hukuncin dana yanke kan shi da Farrah, da ko maganan kirki basayi but kwanakin nan suna magana suna wasa suna tsokanan juna and nasan is a sign Allah ke nunamin I know what I am doing" yay shiru, sanan ahankali yace "bayan abinda yafaru fushin da ni da mahaifiyarshi mukayi dashi yasa yadan

natsu at least bai kara zuwa club ba, akwai mutane danasa ana binshi duk inda yashiga sabida yanzu dakanshi yake driving kar wani abu yakara samunshi yasa bai hiring security personnel sudinga binshi dan har yanzu ban manta cewa akwai people out there dasuke son hurting mini yaro ba, yabar zuwa club ko gidan banza, daga office sai school nasu Farrah kawai yake zuwa haka suka gayamin, yadan fara salla yanzu, yadawo da gemunshi baki, sanan tabama yarage sha sosai though yanasha bawai yadaina bane but yaragu, bansan ko nine ke suspecting nashi ba but I've seen him making advances on Farrah!" Yay dan shiru, ahankali Dad yace "da Zayn yama Farrah wani abu gwara na aurar mishi da ita, she's very young tarayyansu I believe shine sanadin shiryuwanshi dan na nemi zabin Allah kafin nai abin nan, naki fadama Mami dan nasanta bazata taba yarda ba, I know my wife sosai, saisa kaga I am doing this all on my own, kaima I need you to support me" gyadamai kai Uncle yayi yace "to Yaya are you planning on suyi moving zuwa gidansu ko mene" girgizamai kai Dad yayi yace "for now suna gabanmu, we will be monitoring them, Zayn is still 26, inaso nagane menene so, inaso yay developing strong affection for Farrah, yarona baitaba soyayya ba, baitaba son wata ba tunda yake saisa nakeso yaso Farrah matuka ta yanda sonda yakemata zaisa ya chanza, Zayn is a good person idanmu iyayenshi bamu iya mun fito da that good side of him outside ba I believe Farrah can, just trust me" gyadamai kai Uncle yayi ahankali &yace "shikenan Yaya Allah yabada sa'a.

46

12 suka sauka a airport din garin, wasu manyan government cars ne sukazo daukansu da governor Adamawa da kanshi yazo ya tarbi Dad duk gaisawa sukai sosai sanan aka shishiga mota aka kama hanyan akauyen su Farrah da already tuni security personnel sun cika kauyen dan yau sanadin Dad Gwamna zai taka kafanshi a wannan kauyen.
Kusan tafiyan 2hrs yakaisu har kauyen.

Mai gari dawasu manyan mutanen gari ne suka tarbesu sanan aka hadu aka wuce falon mai gari, duk aka zauna kafin kace me mutanen kauye sun taru agaban gidan mai gari ana yada cewa gwamna yazo, saida sukadan natsu sannan Dad yafadi wanda suke nema tukunna da sauri Mai gari ya aika aje akira Malam yazo fada yanzun nan kada yabata lokaci.

Malam na zaune kan tabarma yanacin dafadukan shinkafa da wake dan yanzu rayuwa tai kyau tun kudin da Alhaji yabashi yanzu agarin sune yangayu bayan gidan mai gari, dagashi sai Rakiya ne agidan Inna as usual tanachan gidan nai gari sallama dayaji anata bugawa a kofar gidansu yasa yahakura da abincin yamike yana zura silipas yace "waye, ganinan zuwa" butanshi yadauka yakafa abaki yasha ruwan sanan ya ijiye yay zaure yabude kofa, ganin yaran mai gari Madibbo da babban aminin mai gari yasa yace "ah'ah Tanimu da Modibbo ne, Meya

kawoku nan” Tanimu dake kallonshi yace “munyi manya manyan baki a rugar nan, mai gari na neman ka yanzun nan” dan zaro idanu Malam yayi yace “incedai Lafiya” dasauri sukace “lafiya lau muje ance kada mubata lokaci” gyara riganshi Malam yayi yace “to shikenan muje” yana biyedasu abaya har zuwa gidan maigari dayaga kusan duka mutanen karkaransu agaban gidan ga yan sanda nataresu kada su shiga, suna zuwa yaga anbarsu sun wuce faduwa gabanshi yayi yana tunanin mesukayi, suna shiga falon yaga Alhaji (Dad) da wanan kannin nashi (Uncle) dayama ganinsu yaganesu wani bakin yawu yahadiye yana addu’a Allah yasa badai sun gaji da Farrah sun dawomai da ita bane tunda tabar gidan nan gidan yanzu kaman anjanna more kudinsu suke sunaxin dadi hankalinsu kwance yana zaman lafiya da Inna abinshi idan sun dawomai da Farrah ai yashiga uku, waje yasamu ahankali yazauna duk jikinshi yau wani kalan sanyi yace “barkanku da war haka Alhaji dafatan kun iso lafiya, ince bawani abu Farrah tayi kuka dawo da ita ba”? Yay maganan yana karabin falon da kallo yana neman Farrah, murmushi kowa na falon yayi Maigari yace “ba abinda yakawosu ba kennan, abinda yakawosu yafi karfin wannan” wani kalan yankewa gaban malam yayi yafadi yakara kwalalo idanu yace “tooooh” gyaran murya Dad yayi yace “to Alhamdulillah da Allah yasadamu anan wajen gabaki daya” yadanyi shiru yanadan girgiza kai kafin anatse yadubi gwamna yace “gwamna wato kaga Allah yanada yanda yakeyin abubuwan shine sai yanzu nakara gasgata hakan rabo ne yakawo Zayn wanan gari” murmushi gwamna yayi yace “rabone kam yaron dako hanyan dazaibi yazo adamawa bai saniba balle kauyen kudiri” dan murmushi Dad yayi sanan yakalli Malam yace “Malam kasan nai adopting diyarka abisa ka’ida na shari’a dudda hakan bai dauke cewa amusulunce kaine mahaifinta mai asalin iko akanta ba tunda kaine yayan mahaifiyarta uwa daya uba daya saisa yau natako nazo garin nan domin ka” gyadamai kai Malam yayi yana kallonshi shi kawai kalman dayace yake bala’in tsoronji shine suce sun dawo da Farrah kokuma sun gaji da ita zasu maidota, Allah ka dawwamar da ita achan Malam yay addu’an azuciyanshi.

Anatse Dad yace “Malam namo nemawa yarona daka sani Zayn, wanda diyarka Farrah ta taimakamawa awanan gari, nazo nemama d’ana Auren yarka Farrah idan ka yarda” “waiiii!” Malam yafadi yana goge gumin dake ketomai yashiga murmushi yace “Alhamdulillah Alhamdulillah, yooo Alhaji idan ban baku Auren yarnan ba wayema zan bamawa” yasake washe baki yace “kuda kuka mata sutura sannan ni kawunta ma kukamin suruta ai nafadiwa mai gari shatara na arziki dakukamin dan haka Alhaji amatsayina na jinin Farrah, amatsayina na Kawu kuma Uba awajenta nabaku Farrah, ni so samune ma adaura Auren yanzu kubani sadakinta tunda ga mutane daman makil awaje ko mai gari” Malam yay maganan yana washe baki, mai gari ya gyadamusu kai yana murmushi yakalli Modibbo dake gefenshi yace “jekira Alaramma” dasauri Modibbo yatashi, Gwamna yabada ordwr anshigo da goro biscuit da alawa da abubuwa da yawa wanda yasa aka siyo aka loda a booth din mota tun da safe yau dama, nan aka shiga shigo da abubuwa Dad sai washe baki yake yakalli Uncle dake zaune dunkum kaman dusa yace “ciro wayanka kai video komi” gyadamai kai Uncle yayi yaciro wayanshi, Gwamna yace “abar mutane su shigo” kafin kacema fadan yacika makil wasu awaje wasu ta window, liman yatashi atake aka daura aure tsakanin ZAYN GANUWA && FARRAH MUHAMMAD akan sadaki miliyan goma!.

47

Zaune yake a office din Dad yana sanye cikin wani black suit dayamai kyau bana wasaba idan kaganshi da farko baraka yarda Zayn bane dan he's so concentrating, tunda Dad yabashi aikin nan sai yaune ranan dayasan yazauna ma aikin dan murmushi yayi yadago kanshi dan yagama cikin just how many minutes, hakanan kawai wani kalan faduwa gabanshi yayi dayasa ahankali yakai hannunshi kan kirjinshi yashafa daidai atishawa yazomai dan mikewa yayi tsaye yanabin duka office din da kallo kafin yakalli ogogon bangon office din yaga 1:30 na rana, dan ijiyan zuciya ya sauke sanan yafara tafiya yay hanyar kofa gently yasa hannu yabude kofan sanan yafita, Layla yagani zaune kusada secretary dinsu kallo daya yamata yadauke kai shi baison mace tafiya naci da maita offing nashi abin yake, maida kofan yayi yawuce dasauri Layla tabiyoshi daidai ya shiga lift kafin kofan yarufe ta shige tana kallonshi tace "wai mekake nufi ne batare akace muyi aikin nan ba kullum Saika dinga koroni kana hanani shiga office din" wani matsiyacin kallo yamata sanan ya yatsine fuska kaman badashi takeba wani kalan kulewa tayi hakan yasa tace "wai maisa kacika rainama mutane wayau Zayn eh inamaka magana kamaidani mahaukaciya" wani kalan juyoda idanunshi yayi ya kalleta sannan yadauke idanun abin bakaramin zafi yamata ba hakan yasa tace "wai sabida kazamiyan yarinyar nan Farrah kakemin haka?" Kaman ta tabo wani abu ajikinshi dasauri ya kalleta fuskanshi babu alamun wasa ganin haka yasa tace "yes Zayn, tell me meke faruwa dan bangane maka ba, kai mutum ne dabaka damu da kowa aduniyan nan ba sai kalla, why are you so caring towards that girl, kana fifitani akanta meta fini dashi? Nafita wayewa nafita ilimi nafita kyau nafita karatu, look at me kalli jikina babu abinda zaka nema da bazan iya baka ba, kana marina kanta tell me sonta kakeyi ne are you in love with Farrah Zayn!" Wani kalan bugawa kirjinshi yayi jin kalman so datafadi daidai lokacin sukakai ground floor hakan yasa yabi ta gefenta zai fita hannunshi takama dasauri tafashe da kukan datake rikewa sosai ahankali tace "Zayn please wlh kome kakeso zan baka, I want to be your girlfriend mudinga komi tare har shaye shaye please Zayn" wani kalan juyowa yayi yakalleta sannan yakai hannunshi kan hannunta data daura kan nashi yacire tareda murde hannun idanunshi suna kadawa yace "listen and listen attentively! Karki sake bari wannan bakin naki ya ambato sunan Farrah, and as for this place you can find anybody to work with but forget working with me and lastly" yay maganan yana huci yana matso da fuskanshi dab da nata yana kallon kwayan idanunta yace "I don't f*ck beggars masu rokon maza su cisu naaaa! Zayn yafi karfinki" yakarashe maganan yana jefarda hannunta sanan yajuya fuuuu yawuce mosque abinshi.

Tsugunnawa awurin Layla tayi tana kuka, inhar bazata sami abinda takeso ba to wlh kome Momy keson mishi zata tayata, tanason Zayn yana bala'in burgeta saisa daman taso suyi soyayya suci juna dan Allah ya kera yaron da kyau wlh bata tabayin saurayi kwatankwacin Zayn

ba balle nai kama da Zayn.

Salla yayi dan anriga anyi jam'i tun dazu yana idar da sallan ya jingina da bango yay shiru maganan Layla namai yawo azuciya are you in love with Farrah, son Farrah yake? Ya tambayi kanshi he's trying to compare the thing yanzun nan Layla take kuka wiwi sosai agabanshi babu abinda yaji azuciyanshi saima dada murdamata hannu dayayi yamata warning kan karta sake kiran sunan Farrah, da Farrah ne ke kuka haka daba karamin damuwa zaiyiba, he can't stand seeing her angry, nor sad, wani zubin idan yaganta he just want to tease her dan kawai tamai tsiwa tana zaromai manyan white eyes dinnan nata kaman idan ance ta dakeshi zata iya, he loves seeing her happy and smiling tunda yake baitabajin hakan game da any mace ba koda yay sex dake yaji dadi ba sai Farrah da babu abinda ya tabayi da ita beside ma she's too small, is that what love is? Is he falling in love with Farrah yaya ake gane soyayya? Wayanshi yaciro dasauri yashiga browsing how to know you are in love with someone yadage yana karatun sosai.

"Assalam Zayn!" Yaji anmai magana ana shafa kafadanshi dasauri yadago kanshi wani Indian imam dinsu ne na masallacin nan, yanama Dad aiki ustaz ne sosai, dan murmushi Zayn yamai batare daya amsashi ba, zama Imam din yayi agabanshi tareda lankwashe kafa yasha ganin Zayn company nan ma waye baisan labarin Zayn only yaron Ganuwa ba saidai idan baka company nan, anatse yace "what's the matter Zayn"? Shiru Zayn yayi yana kallon mutumin he's elderly dan akalla yayi sa'an Uncle kuma malami ne nagidi, at least baitabama kowa magana ba outside parents nashi baida aboki yamai magana ne, yay shiru dan murmushi Imam din yayi yace "you can always talk to Me Zayn dudda nasan I am nobody zan iya taimaka maka da shawarwari" yay maganan anatse hakan yasa Zayn yaji kawai ya yarda dashi ahankali yadan cije lips sanan yasaki lips din murya kasa kasa ta yanda kowani yashigo masallacin bazai jisuba yace "Imam I am a bad boy I know you know that cus you work here" yadanyi shiru sanan yace "my parents are not happy with me, I am trying to change but kasan menene matsala na I don't think I can leave without women" yadan yatsine fuska dan iyakan gaskiyanshi yake fadi yace "ni baran iya 2-3days without a woman ba before banama iya one day saida nadawo Nigeria ne nazo nafara koya da kyar murya chan kasa yace what do I do"? Anatse Imam yace "kodai ka dunga azumi kokuma kai aure sabida kadinga samin natsuwa daga wajen iyalinka" dan shiru Zayn yayi yana kallonshi batare dayace wani abuba hakan yasa Imam yace "kanada wacce kakeso"? Shiru Zayn yayi saikuma ahankali yadan fuzarda iska Farrah na fadomai arai yace "I don't know, ni banmasan ko inada wanda nakeso ba all I know is kamin tambayan nan is one person yafado raina Farrah and she hates me cus ta taba ganina da wata" yasake maganan yana yatsine fuska, dan murmushi Imam yayi yasaka hannayenshi biyu yakamo hannayen Zayn anatse yace "yaune rana na farko dana taba zama na magana dakai and all I see was myself lokacin danake da shekarun ka, I was once in your position Zayn duk wani rashinji daka sani nayishi aduniyan nan but rana daya shiriya tazomini sabida question din is menene amfanin been a bad boy can you answer this question Zayn"? Ahankali Zayn ya girgizamai kai,

murmushi Imam yayi yace “is not easy kabar komi da komi tashi daya but idan kai niyya kazo kafara bautama Allah da kyau he will help you, and yama baka the greatest reward by giving you the best woman” yasake murmushi yace “ingaya maka ta yanda zaka gane you are in love with someone Zayn”? Dasauri Zayn ya gyadamai kai, dan murmushi Imam yayi yace “when you care for them genuinely, baka iya jure tsana daga wajensu, u can’t stand hurting them kokuma kaga ana hurting nasu, you love seeing them happy, kuma kawai kaji kanamusu wani kulawa na musamman is love, and if this things are abubuwan dakakeji game da yarinyar daka fadimini tom you are in love with her Zayn” sosai Zayn yake kallonshi yama kasa magana, gyadamai kai Imam yayi yace “tashi ka koma aiki” gyadamai kai Zayn yayi yamike tsaye ahankali har lokacin jikinshi yay sanyi yawuce yakoma office koda yashiga kwanciya yayi kujera yay shiru tunanin Farrah kawai yake yana koran tunanin amman yakasa daina ahaka baiyi komiba yaji ankira la’asar hada tarkacenshi yayi yafito saida yafara ijiye jakan laptop din a motanshi sannan yawuce yatafi masallaci &ana idarwa yafito yashiga mota yawuce.

48

Dagudu yake tuki as usual wani boutique yagani agefen titi da mannequin ansa musu kayan mata masu kyau sosai yaga sunmai kyau hakanan Farrah ne tafadomai arai, he’s trying to stop kanshi but gani kawai yayi yay kwana yay parking gaban shagon yashiga ciki, lafiyayyen english wears yashiga kwasan ma Farrah shirts da wanduna da gowns, yabiya kudi almost 300k masu shagon sai godiya sukemai yashiga motanshi yajawo motan zuwa gida.

Yauma kaman kullum exam din yau yamata dadi, zaune take a falo rikeda iPad din Mami wanda yanzu kusan koda yaushe yana tareda ita tana karatu dashi, Mami na kitchen dudda Farrah taso ta tayata girki kadota tayi tajetai karatun exam, hakan yasa tadawo falo tana zaune ta sanya wata Yar rigan kanti mai dogon hannu baka tanada zanen flowers farare ya tsayamata kasan gwuwanta kanta babu dan kwali sai kalaban data tufke da ribbon baki mai kyau, kaganta zaka dauka wata balarabiya ce zaune akatafaren falon, tana zaune ita kadai akan kujera da iPad din Mami a hannunta tana zane tana kallon zanen Amoeba 🦠 a iPad din tana zanawa da pencil a book din tana koyan lebelling dan gobe biology garesu gabaki daya hankalinta yay nisa a zanen, ahankali aka bude kofan falo aka shigo, Zayn ne yana rikeda katuwan ledan a hannunshi idanunshi akanta saikace tsafi ganinta kawai dayayi dudda ma bata ganshi ba jiyayi zuciyanshi tamai wani kalan sanyi tamai wani wasai now all he needs is tadan kalleshi and get all those her expression akan fuskanta.

Kamshin dataji yadaki hancinta wanda tasan kanshin Zayn kadaine yasa kaman wata Yar bera

tadaina zanen datakeyi, duwawun pencil din hannunta takai bakinta sanan ahankali tadago kanta tareda juyowa hada idanu tayida Zayn daya tsaya yana kallonta kaman baitaba ganintaba ga katon jaka a hannunshi ga jakan laptop a dayan hannunshi yana kallonta, hakanan jitayi gabanta yadan fadi hakan yasa tadauke kanta daga kallonshi dasauri tana zare pencil din daga bakinta cikin kunkuni tace “mutum ko sallama bai iyabama” karasowa gabanta yayi ya tsaya dab da ita dan yanda ya tsaya akanta kafafunta nataba Yadin wandon jikinshi wani iri taji tanaji gabanta nafaduwa hakan yasa taki kallonshi drawing datake yabida kallo yace “look at abinda take zanawa kaman fuskanta” dawani sauri takalleshi zatai magana ya watsa mata mugun kallo yace “kawomin abinci I am hungry” hararanshi tayi ahankali tace “bara’a kawob…….” Daidai Mami nafitowa daga kitchen hakan yasa dasauri tabi ta gefenshi tai hanyar kitchen din tana kara budema Mami kofa da kyau tace “Mami sannu da aiki kawo nakai miki” kafin Mami tahanata ta karbe kulan takai dinning Mami takalli Zayn dayake shirin zama inda Farrah ta tashi tabari tace “kadawo” zama yayi ahankali yana daukan iPad din yace “yes Mami” “kaci abinci” dan yatsine fuska yayi yace “no” tasan dama baicika cin abinci ba hakan yasa takalli Farrah tace “kawomin serving spoon da tray a kitchen” dasauri Farrah tai kitchen ta dauko, seafood pasta da Mami tadafa lafiyayye tazubamai tahada a tray tasama Farrah a hannu tace “gashi kaimai kizo kidauki juice kikaimai ” karba Farrah tayi tawuce tazo ganin yawani kwanta kan kujeran data bari daga iPad dinta harda book dinta yajefar akasa yasa taji ranta yabaci ko kadan Zayn baida manners.
Ijiye tray abincin tayi akasa saida tray yay kara hakan yasa Zayn yadan bude idanu kadan yakalleta yanda tai da manyan idanunta kaman zata cije shi yasa yanuna mata small coffee stool nasu da yatsa in a very lazy voice yace “put the tray on that stool” hararanshi tayi tamike tsaye tana kwashe iPad din da book dinta daya Yar akasa sanan takalleshi cikedajin haushi tace “ina pencil dina”? Lumshe idanunshi yayi ahankali muryanta namai wani sanyi azuciya yana neman sakashi jin bacci, zatai magana daga kitchen Mami tace “idan kin bashi juice din kizo nan Farrah” dawani kalan sauri ta tashi ta ijiye iPad da littafin akan kujera tai dinning fresh juice din da Mami tahada ta dauko da cup suma a tray takawomai har lokacin yana kwance kan kujeran idanunshi a lumshe shima ijiyewa tayi akasa saida tray yay kara tamike tsaye jin baimata magana ba yasa tadan saci kallonshi idanunshi a lumshe kaman ma yay bacci wani irin bacci ne cikin 1min haka. “Did u put the food on the stool ko u are still looking at a fine boy” wani kalan ballamai harara tayi tana nadaman tsayawa ma kallonshi datayi sabida kawai Mami na kitchen yasa tajawo stool din tadauki tray tadaura mai abincin akai sanan tawuce batare data kalleshi ba zuwa kitchen.

Wasu kuloli Mami tanuna mata hakan yasa tadinga daukowa tana kawosu dinning itakuma Mami tafito falon, zama tayi kan one sitter tana kallon yanda Zayn kecin abincin agajiye hakan yasa tace “kagama aikin”? Gyadamata kai yayi ahankali yana kai abinci baki, ahankali Mami tace “babanka yace idan kadawo kada kaje ko’ina kajirashi” Gyadamata kai yayi ahankali yana ture abincin dako 4 spoons baiciba zai tashi Mami tace “koma ka zauna” komawa yayi ya zauna tashi tayi ahankali kaman bataso tazo kusadashi yazauna, plate na abincin ta dauka tace “tun safe ace mutum baici abincin kirki ba kuma yanzu kadan tsakuri abinci kaci zaka tashi bude bakinka” tai maganan tanakai abinci bakinshi dan murmushi kadan yayi ganin tasoma hucewa

da fushin datake wato tsakanin uwa da da sai Allah, ahankali yabude bakin takai abincin yakarba ahankali daidai Farrah nafitowa daga kitchen dauke da kula baki tabude kaman wawiya tana kallon yanda ake bama katon namiji abinci, ahankali takarasa gaban dining ta ijiye kulan sanan tadago tareda juyowa ta rungume hannayenta aciki tana kallon yanda Zayn ke karban abincin da Mami kebashi awani kalan shagwabe, bata taba ganin bad boy irin Zayn ba malalaci sangartaccen banza kawai. Tai tsaki azuciyanta takaraso cikin falon ko kallon inda take batayiba tasa hannunta tadauki littafi ta da IPad din zata juya Zayn yace “pack the clothes naki ne Ke” kallon kayan Mami tayi sanan takalli Zayn din daya dauki glass cup na juice zaisha tace “kaika siyamata kaya” gyadama Mami kai yayi yana kai juice din bakinshi, itama Farrah dan satan kallon babban ledan tayi saikuma takalli Mami, Mami dake kallonta tace “yayanki yasiya miki kaya dauka kiyi godiya” ahankali kaman bataso takaraso tasa hannu tadauka murya chan kasa tace “nagode Ya Zayn” ko jiran reply dinshi batayiba tajuya tai stairs Mami tabita da kallo sannan tajuyo takalli Zayn dakeshan juice abinshi, saida ya kwalwale tass sanan ya ijiye yamike tsaye yana shafa cikinshi ahankali yace “Mami zakisa nafara tara fat ajiki, I am okay” abincin Mami takalla rabi yaci dududu ta tabe baki tace “nidai wuce kaje kai wanka kashirya masallaci” dan juya idanunshi yayi yace “yes Mom” sanan yadauki laptop dinshi yawuce yafita daga dakin Mami tabishi da kallo, she is happy Allah ma yasani dan fushin dasukayi dashi &na kwana biyu yasa yadan natsu Allah yasa natsuwan ya dore haka.

49

Around 7 Dad yashigo gidan shida Uncle, Uncle na shigowa motanshi yawuce yace “Yaya nawuce gida saida safe” binshi da kallo Dad yayi yace “don’t forget to come early gobe duk kayi wani iri jeka kahuta” Dad na maganan yay hanyar flat din Mami burinshi duk inda zaije yadawo kawai ya sauka dakin Mami dan yasan zai sami lafiyayyen abinci da ita tagirka daki mai kamshi dayaji kamshin turaren wuta ko kwayan datti bazai taka ba, sannan ita kadai ke komi nata sai yanzu da Farrah ke komi dudda haka bata barinma Farrah girkin dazaici saidai suyi tare, da sallama yashiga falon wani lafiyayen kamshi yadaki hancinshi babu kowa a falon hakan yasa yawuce sama dakin Mami yabude tana kan dadduma hakan yasa yay murmushi yawuce dakin Farrah dashima yabude da sallama itama tana zaune kan dadduma murmushi yayi yawuce dakinshi wanka yayi yafito ya shirya cikin jallabiya fara kal sanan yadauki charbi yabude kofa yafito daidai Mami na shirin shigowa dakin ganin yasa tace “zaka masallaci” Gyadamata kai yayi yace “eh kaimin abincina sama nadawo asama zanci abinci nai sauri kada jam’i yawuceni” yay maganan yana wucewa hakan yasa Mami itama tawuce saida tafara bude kofan dakin Farrah ganinta tana salla yasa tasauka kasa abincin Dad takaimai dakinshi sanan tawuce dakinta.

Ana idar da salla yadanyi azkar kadan sanan yatashi gamamakin shi Zayn yagani a sahun farko inda yake yana zaune yay shiru wani tattausan murmushi yasaki sanan yajuya batare dayamai magana koyama bari yaganshi ba yafito yawuce gida, a falo yaga Farrah zaune da littafi a hannunta tana ganinshi ta ijiye littafin tana murmushi tace “Dad sannu da zuwa, Dady ina kaje banganka yau” dan dariya yayi yana karasowa inda take kanta yashafa cikeda wasa yace “garinku naje yau” zaro idanu tayi tana murmushi zata karamai tambaya yace “yi karatu kije ki kwanta you have exam tommorow yarinya na” murmushi tayi tace “Dad daman sabida kai na sauko kasa naganka idan kadawo nagama yanzu zanje na kwanta, Dad nagaji yau banyi baccin rana ba saida na koyi all the drawings da labelling nasu” baki Dad yatabe yace “Allah yasoni banyi science ba” Mami data fito daga kitchen rikeda jug tace “saisa kai missing ai” Farrah tahau dariya itama Mami na dariya Dad yace “Au taron dangi zakumini keda diyarki Allah yasoni nima inada Zayn dina shima dan art ne kaman babanshi” tashi Farrah tayi tace “Mami bacci saida safe” Mami tace “mu kwana lafiya sarkin baccin wuri, muje Alhaji kaci abinci” tashi Dad yayi yabi Mami zuwa daki, saida yaci abinci yay nak sannan takwaso komi tafito dashi zuwa kitchen sannan tadawo dakin zaune taga Dad bakin gado gefenshi yanuna mata hakan yasa tamaida kofan ahankali tarufe takaraso ciki anatse ganin kaman akwai abinda yakeso yafadi mata ta sauka kusa dashi.

Dan ijiyan zuciya yasauke ahankali sanan yakalleta kafinma yay magana Mami tace “menene Alhaji? Talk to me please” dan shiru Dad yayi yana kallonta, ahankali yace “I don’t really know yanda zaki dauki abinda I’m about to tell you right now Dan kinsha fadi cewa I am the only one nake taking decision in Zayn’s life tun yana yaro gashinan kuma yanzu ma still nine ke taking decision din dan nayi wani abu yau wanda bansan yanda zakiyi accepting nashi ba” Dad yay maganan ahankali yana kallonta ganin yanda ta natsu tana kallonshi kanaganin fuskanta babu komi cikinshi sai tambayoyi dasonjin mekuma yayi yau, dan lumshe idanu yayi sannan yabudesu murya chan kasa yace “nama Zayn aure yau din nan!” Wani kalan sauka maganan yayi a kunnen Mami kaman saukan aradu hakan yasa dasauri ta kalleshi trying ta gasgata shine yafadi maganan ko kunnuwanta ne sukaji akasin hakan, gyadamata kai yayi yace “yes wife na aurar da Zayn yau dazu misalin 1:30 na rana” wani kalan kallon mamaki Mami kema Dad dayasa bakinta ma yakasa motsi sai kallonshi da kawai takeyi, murya chan kasa kasa kaman Dad baiso yafadi yace “na auramai Farrah!” Wani kalan mikewa tsaye Mami tayi azabure tana kallon Dad dake zaune bakin gado yana kallonta ahankali tana numfashi da sauri da sauri kirjinta na bugawa fast fast takasa magana, ahankali Dad yamika hannunshi yakama hannun Mami dake bar bar yace “I know how you must be feeling right now Wife, nasan inda na gayamiki ba lallai kibani goyon baya ba saisa I went ahead ni da uncle da gwamnan Adamawa with some top officials muka tafi garin, Baffan ta yabamu Auren akan sadaki 10M agidan mai gari which kusan all the people na kauyen sun shaida auren video daurin Auren yana wayan Uncle ma” yanda ran Mami taji yana baci har wani duhu duhu take gani, cikin karason ta gasgata abinda taji tanuna kofa tace “Alhaji you mean this Farrah, Farrah na ka aurama Zayn, ita Matar Zayn ne yanzu”? Gyadama Mami kai Dad yayi a natse yace “eh, Zayn dinmu mijin

Farrah ne yanzu" tunda ta auri Alhaji bata tabajin yamata abinda yabata mata rai ba saiyau kallonshi tayi ido cikin ido tace "Alhaji sabida ba kaine ka haifi Farrah ba is that why kamata Zayn a matsayin miji"? Wani kallo Dad yake mata dan baigane kan tambayanta ba cikin fushi sosai Mami tace "yes I mean my question sabida na tabbata Alhaji inda munada diya mace wani yazo neman aurenta mai hali sak irin na Zayn bazaka taba yarda kabata  Zayn ba sabida ba kaine ka haifeta ba ko? Alhaji lemme tell you this dakayi adopting Farrah kabani ita Allah shine shaidata na dauki yarinyar nan amatsayin yarna nai nakudanta na wata tara nakuma haifota batada banbanci da Zayn a idanuna kuma bazan tabaso diyata ta auri namiji mai hali irin na Zayn ba, wani kalan shaye shaye ne Zayn bayayi tell me?!" Mami tama Alhaji ihu dabata tabamai ba, cikin tsananin fushi tace "do I need to tell you Farrah is just 18, that girl batasan namiji ba, she don't know anything Zayn akwai kalan macen dabai sani ba aduniya eh? Akwai kalan matan that Zayn did not sleep with, did you even know your son health statu……." Tashi Dad yayi ranshi abace yadaga mata hannu yace "ya isa hakanan dena batamin image din yaro stop talking kaman yarona nada HIV ko wani abu naga ko lokacin da yake asibiti kinsa andebi jininshi anmai General test baida any cuta" cikin balain ihu tace "daga lokacin zuwa yau can you account how many women did he sleep with? Alhaji why are you selfish maisa zaka cutarda rayuwan Farrah ta hanyar auramata Zayn is it because you are not her biological fathe………" "Wife!" Yadaga hannu kaman zai mareta hakan yasa tai shiru tana kallonshi hawayen dasuka zubomata ta sharesu yace "yanda kika dauki Farrah as diyarki I took her nothing less than that, bazan taba cutar da Farrah ba ke kinsanni saidai ki Bawa mutane labari waye ni yaya nakeson yarana, I agree nasan halin Zayn all you stated babu wanda bayayi amman waya gayamiki mutum baya chanzawa? Kinsan karfi da ikon mace akan namiji? Behind every successful man is a woman, you might see Farrah karaman yarinya but kada kiyi mamaki itace silan shiryuwan danki, yanzu dazaran yasan yanada mata an killacemai agida waya gayamiki zaibi na waje? I thought bayan nafada miki good news dinnan zaki sama Auren albarka kimusu addu'a why all this negative thought"? Baki Mami tabude zatai magana yanuna mata kofa yace "please kitafi dakin ki yara dukansu biyun nawane nine ubansu nikuma na yanke hukunci idan kinga dama kisa albarka ko kada kisaka ni nasaka nawa nagode" yana maganan yahau gado tareda danna switch yakashe wutan dakin yanajan bargo, Mami tadade tsaye awajen sannan ta share hawayenta tass, anatse tace "naji yara nakane, I have one request kada kafadama Farrah koma menene kabari tagama exam ranan Friday" tana maganan tabude kofa tafice daga dakin Zayn tagani tsaye turus agaban dakin idanunshi sunyi ja, ko kala bata cemaiba tawuce fuuu tashiga dakinta yabita da kallo ta maida kofanta tarufe.

Maida fuskanshi Zayn yayi yakalli kofar dakin Dad sannan ahankali yaja kafarshi da kyau zuwa gaban dakin yabude yashiga ciki tareda saka hannu yakunna wutan dakin hakan yasa Dad yadago dasauri ganin Zayn yasa ya tsaya turus batare dayay maganan dayakeso yayi ba, ahankali Zayn yakaraso gaban gadon Dad ya zauna yana kallon Dad, baki Dad yabude zaiyi magana kawai Zayn ya rungumeshi tsamtsam very tight, mamakin runguman Dad yayi amman dudda haka samin kanshi yayi da rungume yaron nashi back he really missed his son, murya chan chan kasa Zayn yace "Papa I love Farrah!" Dawani kalan sauri Dad yadago Zayn daga jikinshi yana kallon fuskanshi kaman Maison gasgata wani abu, gayadamai kai Zayn yayi

abunku da yaran zamani basusan meye kunya ba, yace “Dad I really love her, I always think of her, I hate to see her cry or hurt, I love seeing her happy, Papa I am in love with her she’s my Angel” wani kalan kyalkyacewa da dariya Dad yayi yana kallon fuskan Zayn din ganin yanda yafadi komi da zuciya daya babu karya aciki, dan sosa kai Zayn yayi yadan yatsine fuska yace “why are you laughing Papa what’s funny”? Hadiye dariyan Dad yayi yajawo Zayn jikinshi kaman wani dan yaro yace “sabida bantaba zaton zaka so wata aduniyan nan ba ayanda naganka yanzu daka fadamini kanason Farrah half of my problem has been solved” kallonshi Zayn yayi yace “Dad dagaske kamana aure”? Gyadamai kai Dad yayi yace “yes Zayn na aura maka Farrah, she is your wife halak malak” wani kalan murmushi Zayn yayi yace “you are the best Papa in all the 7 planets”  dan dariya Dad yayi yace “kaga your Mom is not happy with the marriage I want you to prove her wrong, yanzu kanada mata so start being responsible, all halayen nan kazubar dasu na samari ne, pray on time, babu zuwa club yanzu da shaye shaye, banda mata Zayn kaji tsoron Allah yanzu kanada matanka halas malak, banda shan taba sannan karike salla, and work on relationship dinka da Farrah make her love you though bazan fadamata komiba yanzu sai tagama exam, ka natsu banso kabama mamanka any hujjan dazatace gashinan abinda tafadi kaji” gyadamai kai Zayn yayi Dad yace “I got you for life yarona kome kakeso will always be yours” wani kalan murmushi Zayn yayi yama rasa ina zai saka kanshi kaman yazare yakeji dan dadi yamike tsaye yace “Dad lemme go and check on my wife” sauka Dad yayi daga kan gado kaman munafuki yace “but kada kadade adakin kada mamanka takamaka” yay maganan yana rakashi bakin kofa saida yafito sannan yace “i maza kaje” dasauri Zayn yay hanyar dakin Farrah tareda saka hannu yabude kofan ahankali yashige Dad sai murmushi yake kaman anmai kyautan makka.

Jama’a wannan& wani kalan Dad ne😂😂😂😂😂

5⃣0⃣

THIS BOOK IS NOT FREE❌
Wanan littafin FARRAH 500 ne kacal.
Don magana dani M SHAKUR chat me up directly by clicking on this link;
wa.me/+2347012181461

The Wellness by Oriflame routine is designed to support your intake of protein, dietary fibre and

micronutrients, in the right proportions, every day.

A = ACTIVATE
Set the foundation of your routine with vitamins, minerals and omega-3 fatty acids. These are needed every day to fill the nutritional gaps in your daily diet. You find them in our Wellness Multivitamin and mineral.

B = BUILD
Boost your defence system, and even build it over time, with the amazing Astaxanthin, together with bilberry extract and protein. Antioxidants are your active defense against environmental pollutants and help your body cope with a hectic lifestyle. Proteins help your body build new cells. You can find these in our Wellness Shakes.

C = CUSTOMISE
We all have individual needs depending on our age, lifestyle and general wellbeing. That's why you should top up your routine with additional nutrition to feel and look your best. This includes using products like our Wellness soups and bars.

Meanwhile lemme all introduce you to supplement da I think we be solution to all problems na jikinmu.

Dukanmu nan munsan ORIFLAME is a reputable brand da aka sansu wajen wallafa abu mai kyau yanzu sunyi Supplement mai suna WELLNESS by ORIFLAME.
Kowa dakuka gani mata da maza muna bukatan some mineral, vitamins da sauransu dazai helping jikinmu da system namu, supplement dazai karama defense mechanism namu karfi to protect us from ciwake ciwake, sanan dazai taimakawa organs dinmu yin aiki da kyau.

Idan kina shan wellness zaki kyau, zai karamiki lafiya, zai taimakawa organs naki sosai, akwai so many reviews, wata tace tunda tasha wellness tafara samin ruwa gaba, wata tace skin nata yay fresh, wata tace gashinta daya karairaye yadawo, wata tace nonon ta yakara cikowa, banda haka wellness na bada kariya against cancer.

Wellness is the best supplement da ake dashi right now wanda kasashen duniya da dama sukasha kuma suke recommending ma mutane.
❤️
Maida kofan dakin yayi yarufe ahankali without making any sound yajuyo yana kallon cikin dakin dudda baya ganin anything dan dakin duhu sai sanyin AC dakuma kamshin turaren wuta da dakin keyi dake neman tsagamai kai da dadi danshi dakinshi kamshin turarukan shi suke amman basa taba kamshin turaren wuta dan ba'a kunna mai, kin kunna wutan dakin yayi gudun karya tadata tamai wannan ihun tsiwan nata Mami taji ya shiga uku, hannunshi yasa yashiga

tattaba jikin wandonshi yana neman wayanshi yama manta inda wayan yake tsabagen yanda yakejin dadi jin babu wayan a aljihun wando yasa yatuna yana aljihun gaban riganshi dasauri yakai hannun nashi wajen yaciro wayan ya kunna flash din wayan tareda haska dakin, he thinks this is the first time yake shigowa dakinta ko'ina na dakin fesfes, ga kayayyakin daya sayomata gabaki daya tacirosu ta linkesu suna kan study table dinta, ahankali ya haska kan gadonta tana kwance daga ita sai wani rigan bacci sky blue mai hannun taliya da gajeren wandonshi daya tsayamata a gwuiwa ta kanannade, fuskanta gabaki daya yanakan littafin datake zanenta aciki iPad din Mami yafadi akasa tareda pencil dinta da byro, dan murmushi kadan yayi ahankali yace "stubborn gurl" cigaba dabin dakin yayi da kallo yafara tafiya ahankali yana kallon ko'ina yakarasa zuwa gaban bathroom nata yabude bayin yayi ahankali yana kallo, bra dinta yagani white da white pant ta wanke ta makalasu ajikin wani cute hanger na bayin, wani kalan murmushi yayi ahankali yakai hannunshi yakama bra cup din wani kalan lumshe idanu yayi sanan yazare hannun yabude cupboard dake bayin babu komi ciki sai pads dinta na koltex masu kyau sosai ta jerasu zaka dauka danki dasu tayi, maida cupboard din yayi yarufe sannan yajuya ahankali yafito daga bayin yana kallon komi na dakin sannan yakaraso gaban gadon ta ya tsugunna ahankali wayanshi yadaura kan side drawer sabida kada yadinga haska mata fuska direct, juyowa yayi yakalli fuskanta daduk yarufe da kitsonta gently yakai hannunshi yadaura kan gashin ahankali yadage kitso yamaidasu baya hakan ya bayyana fuskanta dayay fayau tana bacci innocently baisan mesa ba sai yanzu yaji yamafi da sonta dayaji she's his wife, hannunshi yakai gently yadaga kanta tareda jawo Littafin da fuskanta kekai sannan yamaida kan nata ya ijiye kan gado dan yatsine fuska tayi cikin bacci tana turobaki murya chan kasan makoshi tace "Mami nasha maganin" murmushi yayi kaman tana jinshi yace "karya wani magani kikasha" ahankali yakai hannunshi yadaura akan kunnenta yana kallonta kaman yaune rana na farko yafara ganinta dan lumshe idanu yayi yasa hannu yaja bargon gadon yarufa mata baiwani so yakalleta sosai yana murmushi sanan gently yamike tsaye zai wuce hannunshi yaji anrike dasauri yajuyo yakalleta itane tarike hannunshi cikin bacci, hannunta are so warm kaman ba itane ke cikin AC ba, sake dukowa yayi yakai hannunshi kan very soft kumatunta yace "do you want me to sleep here Angel"? Janye hannun yayi sannan yamike tsaye yana kallonta remote yadauka yarage karfin Ac sannan yabude kofan ahankali yafito tareda maida kofan yafito yana murmushi yawuce yasauka kasa yafita daga dakin yawuce side dinshi, raLnan da kyar bacci ya daukeshi sabida yanda yake farin ciki.

5️⃣1️⃣

THIS BOOK IS NOT FREE❌
Wanan littafin FARRAH 500 ne kacal.
Don magana dani M SHAKUR chat me up directly by clicking on this link;
wa.me/+2347012181461

The Wellness by Oriflame routine is designed to support your intake of protein, dietary fibre and micronutrients, in the right proportions, every day.

A = ACTIVATE
Set the foundation of your routine with vitamins, minerals and omega-3 fatty acids. These are needed every day to fill the nutritional gaps in your daily diet. You find them in our Wellness Multivitamin and mineral.

B = BUILD
Boost your defence system, and even build it over time, with the amazing Astaxanthin, together with bilberry extract and protein. Antioxidants are your active defense against environmental pollutants and help your body cope with a hectic lifestyle. Proteins help your body build new cells. You can find these in our Wellness Shakes.

C = CUSTOMISE
We all have individual needs depending on our age, lifestyle and general wellbeing. That's why you should top up your routine with additional nutrition to feel and look your best. This includes using products like our Wellness soups and bars.

Meanwhile lemme all introduce you to supplement da I think we be solution to all problems na jikinmu.

Dukanmu nan munsan ORIFLAME is a reputable brand da aka sansu wajen wallafa abu mai kyau yanzu sunyi Supplement mai suna WELLNESS by ORIFLAME.
Kowa dakuka gani mata da maza muna bukatan some mineral, vitamins da sauransu dazai helping jikinmu da system namu, supplement dazai karama defense mechanism namu karfi to protect us from ciwake ciwake, sanan dazai taimakawa organs dinmu yin aiki da kyau.

Idan kina shan wellness zaki kyau, zai karamiki lafiya, zai taimakawa organs naki sosai, akwai so many reviews, wata tace tunda tasha wellness tafara samin ruwa gaba, wata tace skin nata yay fresh, wata tace gashinta daya karairaye yadawo, wata tace nonon ta yakara cikowa, banda haka wellness na bada kariya against cancer.

Wellness is the best supplement da ake dashi right now wanda kasashen duniya da dama sukasha kuma suke recommending ma mutane.

Da asuba as usual kafinma Mami ta tadata ta farka bude idanunta tayi ahankali tana kunna wutan dakin batasan mesa ba but hakanan kamshin turaren Zayn taji yacika dakin dan tabe baki tayi ta harari kayan daya siyamata data daurasu kan study table dinta sannan ta sauka

